[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: https://chat.whatsapp.com/DgTUlodRcp2AHM4rmfKTqK
[10/21, 2:54 PM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU.

By

CHUCHUJAY ✍🏾

EPISODE1️⃣

KIRIKIRI MAXIMUM PRISON LAGOS STATE NIGERIA.

A kullum zaryarta zuwa prison ɗin yana mutuƙar bata mata rai ,
Bata jin wani tausayi ko rashin jin daɗin abunda yake faruwa da shi duk da irin ɗinbin san da tayi masa a baya,

Ta sa a ranta akan cewa kaddarar sa ce,duk wani wanda zai nuna mata rashin dace wa akan bibiyar sa Ya bata takardar sakin ta Kallansa kawai take sannan bata sawa a ranta domin ta gama yarda da yarda ɗan Adam yake da hallayyarsa,

Cikin handcuff Dukkan hannayen sa biyu Haka aka rako sa ,kallan sa kaɗai yakan sa mata faɗuwar gaba ,hakazalika a yanzu haɗa ido kawai da tayi dashi sai da Taji mumunar faɗuwar gaba Ta kawo mata ziyara,
Abubuwan da suka faru tsakaninta dashi take suka fara tariyo mata ,danne su tayi dan tafiyar su babu abinda ya haifar mata sai tashin hankali da dana sani,
Kallanta ta mayar gareshi dan ta gama yarda a yau sai tabar kirikiri da sakinsa akanta,
Glass Mai Kauri ne tsakaninsu Wanda yake ɗauke da bulloli Shida,telephone ɗin dake sakale a gefenta ta ɗauka ta kara a kunne yayin da shima yayi halkan,

Magana ta fara "Hafiz nazo ka bani takarda ta dan Allah mu daina bata lokacin juna kodan zaman mu na farko kan ka chanja Mai ɗan dadi duk da yaudara ne, ka sakeni dan koda ace huƙuncin ka ba kisa bane ta hanyar rataya ,koda kuwa ace za'a cire duk wani charges akan ka,Hafiz bazan taba sake zama da Kai ba.

Kukan da yasa shine abunda yayi mutuƙar bata mamaki,tasan wanene hafiz mutum ne Mai mutuƙar juriya da jarumta ,amma a yau yana mata kuka dan kawai tana masa maganar Ya sake ta,
Shiru tayi tana Mai jin kukan nasa ta cikin telephone ɗin a yayin da yake ratsa dukkan wani sasshe na jikinta,
Ina ma hafiz bai zabi tarwatsa rayuwarsu ba ,ina ma ba'a kamasa da laifuka mafi munin wanda aka kamashi dashi ba,
Ina ma!
Tana kokarin cire telephone ɗin dan bazata iya cigaba da jin kukansa ba ta tsince muryarsa yana cewa"UMAIMAH dan Allah dan Annabi kar ki takura mun na sake ki,ni mutum ne Mai laifuka da dama a wajen ubangiji, kila yamun Rahma sakamakon mutuwa da zanyi a matsayin mutum mai Aure,"Ke mutuniyar kirkice UMAIMA ,a dukkan rayuwata ban taba Auren mace Mai kamala da haƙuri ba kamar ki,ke maratussalaha ce ,ke macece yar Aljanna,Mai tausayi da jin kai,dan Allah UMAIMAH kimun wannan Alfarmar guda ɗaya duk da kuwa ni Azzalumine a wajenki.

Bata san lokacin da ta kwace da wani irin kuka ba Mai mutuƙar cin rai,
Take duk ikirarin da take na rashin jin tausayinsa Ya kau dan ta tabbata koda a ce babu soyayyar sa a tattare da ita tasan tabbas yana da soft spot a wani gurbi na zuciyarta,
Tana kokarin cire telephone ɗin yace"UMAIMAH bana so na mutu,Ina mutukar tsoran zuwa na haɗu da mahaliccina,bana so umaimah ,Ina san na rayu na dai dai ta tsakanina da ubangijina na rayu da ɗana wanda shi kaɗai Allah Ya bani,sannan babban farin cikina ta tsatsanki Ya fito,"Amma kash kaico na ,bani da wata damar ,nayi wasa da wadda Allah Ya bani ,nayi fatali da kyautar ni'imar da yayi mun saboda san zuciya da kwaɗayin duniya wanda a yanzu Ya kaini Ga dana sani,
UMAIMA gobe za'a rataye ni ,gobe zan mutu,babban tsorona kenan,a razane nake da Ya zamana nasan ranar mutuwa ta.

Shiru tayi tana Mai kallan sa ta glass d'in da Ya rabasu,hannunta tasa ta dafa glass ɗin a dai dai inda Ya ɗora hannunsa ,
A hankali ta shafa tana Mai tuna yarda ya nuna mata soyayya kamar zai cinyeta a wata biyu na Auren su,

Lumshe idanunsa yayi wanda suka faɗa saboda tsantsar masifa yace"kar ki bawa ABDALLAH labarina idan Ya girma,bana san yasan babansa failure' ne a rayuwa sannan na yarda da zaki bashi tarbiyya Mai kyau,kar ki barshi Ya rabi dangina dan na bar miki shi halak malak,dangina ba mutanen da zanyi Alfahari dasu bane Kema kin sani sune mafarin jefani cikin wannan masifar,ina so idan da dama ki raini ABDALLAH Ya zama cikakken Mahaddacin Qur'ani ,Ya zama malami akasin mahaifinsa,"
Idan Kinje gida a side drawer dake gefen gadona na aje cheque na milliyan goma ,ki ɗauka ki juya ma ABDALLAH ,wallahi tallahi ba ta hanyar banza na samesu ba,kuɗi ne masu tsafta babu gurbaci a cikinsu,
Kisa Abdallah yana mun Addua ,Kema idan har da dama zan samu a gurinki bazan ki ba, duk da nasan abun zaiyyi wuya duba da yarda na cutar dake a rayuwa.
Ina mai mutuƙar baki hakuri akan ki yafe mun,Allah Ya baki miji Umaimah wanda yake salihi, Ina Mai miki addua ki Auri miji nagari ba irin mazajen da kika AURA GUDA UKU BA.
Allah Ya haɗa fuskokinmu da Alheri.
Nagode Allah yayi miki Albarka.

A Yarda ma'aikatan suka kawo sa haka suka ƙara tasa keyarsa dan komawa da shi kurkukun da suka dauko shi,
Buga glass ɗin tayi wanda hakan yasa shi tsayawa,ma'aikatan basu ja ba dan sukan bawa wanda yayi expire dama duba da duniyar ma barinta zaiyyi baki Ɗaya,

Roban take away ta ɗauko daga jakarta wanda bata san dalilin da yasa ta zo dashi ba,ɗaya daga cikin ma'aikatan ne Ya zagayo Ya karba,Ya juya zai tafi tace masa"ka faɗa masa Na kawo masa favorite dambun naman kazan da yake so sannan ni na soya,sannan insha Allahu indai na dena masa Addua to numfashina ne Ya yanke daga jikina,sannan zai Alfaharin abunda zai tafi Ya bari."

Wani irin kuka ta fashe dashi a yayin da taga yana mata murmushi lokacin da aka aika masa da Saƙonta,da sarsarfa ta tashi tabar gurin tana Mai Kallan yarda aka maidashi har a lokacin murmushin na akan fuskarsa,

Kuka take sosai a motarta tana Mai jin wani irin zafi a cikin kirjinta,tabbas rayuwar Hafiz babbar Aya ce ga mutane .

WACECE UMAIMAH ?

DR UMAIMAH USMAN BULAMA,
Ƴa ɗaya tilo a gurin Amaryar Alhaji usman bulama,
Alhaji usman bulama mutumin Zaria ne wanda zama Ya kaishi garin ADAMAWA YOLA garin FULANI tushen kunya,
Alhaji Bulama sharraren mai kuɗine wanda ake lissafawa a cikin dumbin masu kuɗin duniya ba kasa kawai ba,
Architecture ne wanda Allah ya habaka a hanyar domin irin tsabagen basirarsa,
A irin buɗin da Allah yayi masa har Construction  company (BULAMA CONSTRUCTION COMPANY) ne dashi wanda suke samun kwangiloli masu dama wadda sai da rabanka ma suke karba.

Matan Alhaji bulama biyu,hajiya zuwaira itace uwar gida wadda ta haifa masa yara huɗu dukka maza babu mace ko daya.

Mutane kance soyayya da sa rai da yayi ga ɗiya mace ne ya sashi ƙarin mata amma a zahiri kuwa ba haka bane,
Soyayyar Bafulatana Nana Surbajo dake yawan kawo nono Companin sa ita tayi masa mugun kamu duk da kuwa yanayi kamar bai taba kula da ita ba a yayin da ita bama tasan yanayi ba duba da shi ɗin mutum ne da ganinsa sai ka cike Paper.
Da yake Allah Ya kaɗara matarsa ce bai kasa a gwiwa ba wajen bincike akanta inda Ya gano daga rigar da take yaje ma iyayenta da maganar Aure tun kan Ya furta mata soyayya.
Iyayenta ba masu tsaurin ra'ayi bane dan haka suka bashi dama Ya nemi soyayyar nana surbajo duk da yarda danginsu suka masu Cha akan zasu bama dan yankan Kai diyarsu tilo.
Ba wani wahala Ya sha ba Ya samu Auren surbajo wanda kwata kwata baiwa uwargida zuwaira daɗi ba amma babu yarda zatayi da yin Allah dan haka abun ya kullu yarda Allah yaso.

A shakara Allah Ya Azurtasu ɗiya mace wadda taci suna UMAIMAH,sosai Alhaji bulama yayi mutuƙar murna wadda tasa shi fitar da zakka Mai mutuƙar tsoka,

A duniyarsu ta shahararrun masu kuɗin babu wanda bai san da samuwar UMAIMA ba da kuma irin Adadin ƙaunar da yake mata dan baya iya boyewa,
Wannan ƙaunar da yakewa UMAIMAH ba karamun  damun hajiya zuwaira take ba da yayanta uku, cikin yaranta Abubakar,usman,umar,Aliyu,Abubakar babban danta ne Kawai yake

jin Umaimah a cikin zuciyarsa kamar uwa daya suka fito amma sauran kuwa ba karamun saka masu kiyayyar umaimah da uwarta tayi ba.

A haka umaimah tayi ta girma cikin soyayya da kulawa duk da kuwa irin tsangwamar da take sha gurin uwar gidan Alhaji bulama da yaranta uku,
Tun kafun tasan menene kiyayyar har ta fara ganewa tasan mema kiyayyar ke nufi.

A lokacin da ta shiga shekara goma sha biyar Allah yayi ma mahaifiyarta rasuwa sakamakon brain cancer da ya sameta,babu irin kudin da Alhaji bulama bai kashe ba dan kawai Nana surbajo ta warke amma abun yaci tura,
Tun rasuwar Nana surbajo Umaimah ta ci buri kuma ta sawa ranta sai ta zama surgeon,
Da wuri ta fara makaranta sabida irin kaifin kanta,tana da shekaru goma sha biyar ta kammala karatun secondary school ɗinta ,
A shekarar da ta zagayo ya kai ta harvard university inda ta fara karatunta na liktanci,
Babu irin kauɗin da hajiya zuwaira batayi ba akan Kai umaimah Harvard da akayi amma yayi kunnen uwar Shegu da ita, umaimah na shekara ta uku a Harvard mahaifinta yaje Ya ɗaukota, Bata tambayesa dalili ba d'an tasani idan da wanda yake san cigaban ta bai wuce shi ɗin ba sannan ta yarda duk wani decision da zai yanke akanta mai kyau ne.

Bayan dawowarta Nigeria tayi mutuƙar mamaki da taji wai ansaka ranar Aurenta da Habib Aliko yaran Aminin Daddynta,
Koda Daddynata yayi mata magana akan Aurenta da Habib nuna wa tayi duk abunda Ya yanke akanta dai dai ne muddin karatunta bazai tsaya ba,
Tasani Daddynta Ya chanza amma bata saka wa ranta komai ba,baƙaramar rawa Hajiya zuwaira ta taka na wajen Auren Umaimah da Habib d'an ita ta haɗa komai.

Yaya Abubakar kaɗai ke bata baki yana Mai nuna mata Auren ma ba matsala bane sannan bazai shiga rayuwar karatunta ba tunda Daddy Ya jaddada ma Habib d'a mahaifinsa kan zata cigaba da karatun ta and baya buƙutar su ɗauki nauyi zaiyyi komai,
Haka nan ya Auri Habib inda Ya ɗaukota daga garin adamawa ya kawota kano,
DE ta samu a TURKISH MEDICAL SCHOOL inda ta dora daga inda ta tsaya.

Tun ranar da aka kaita gidan HabIb tasan ba mijin Arziƙi bane 'dan a buge ya shigo ,bai tsaya anan ba kuma a ganawarsu ta farko raping ɗinta yayi wanda yaji mata ciwo sosai,tashin hankalinta bai fara ba sai da tasan Habib manemin mata ne sannan kuma ɗan giya ,bata sanar da kowa ba take zaune dashi a Haka musamman da taga yarda Daddynta ke mutuƙar yaba hankalinsa 'dan munafukine na masifa saboda baya taba nuna shi 'dan iskane gaban iyayenta,a Haka har rabo Ya shiga tsakaninsu ta haifa masa yaro na miji wanda yaci suna NAMEER,
NAMEER na da shekara ɗaya Habib ya saketa sakamakon dawowa da yayi gida a buge suna zaune da NAMEER a falo 'dan kawai tayi faɗa da mita akan Ya daina shigo musu gida muddin giya bata sake sa ba,
Cikin maye Ya mata saki uku wanda a musulunci ma ta saku,
Daga baya Ya dawo yayi ta naci akan shi bai saketa ba amma Daddynta yayi masa koran

kare sannan Ya ƙwaci NAMEER ɗin da Ya kwallafa rai akai wanda mahaifin Habib bai jaba 'dan baya san alaƙarsa ta baci da Alhaji Bulama.

Kamar wasa bayan iddarta Daddy ya sake introducing mata BILAL shima dai yaran Abokinsa,
Abun ne Ya dameta duba da Ko Auren ta na fari bata gama Alhini akai ba amma wai Daddyn Ya kawo maganar Auren ta da wani,wanda shima kamar Habib ba sanshi take ba,
Kuka ta ɗingawa Abubakar Akan ita bata san Auren Bilal 'dan Auren ma bata so baki daya ,she's just 21 amma ace wai har Zatayi Aure na biyu,
Baki abubakar yayi ta bata akan zai je ya samu mahaifinsu yayi masa magana,
Koda yawa Daddyn nata magana sai cewa yayi Ai hajiya zuwaira taje wajen malaminta dake mata Addu'a Ya tabbatar mata muddin Umaimah ta zauna babu Aure zata lalace kuma babu wata nasara da zata tabayi a rayuwa shi kuma bazaya taba barin ɗiyarsa tilo guda ɗaya ta tagayyara ba,
Kara yarda yayi da  Lallai daddy yana san umaimah to extent that yama rasa inda zaisa Alƙibilar tunaninsa,'dan ko shi da yake ɗan Umma yasan maganar ta ba dai dai bane duba da kalar tsanar da take wa UMAIMAH ɗin ,kawai dai tace tana so ta bar mata gida,
Kara bawa umaimah hakuri yayi a karo na biyu inda ta yarda da Auren BILAL wanda yake da mace ɗaya,shima kuma mazauninin garin kano 'dan Haka Ta dora karatunta inda ta tsaya.

Duk da tarin kuɗin mahaifinta hakan bai hana kishiya da miji da uwarsa galaza mata ba,gida ɗaya suke baƙi dayansu,
Karatun ta ne basu so amma kuma babu yarda zasuyi dan basu suke ɗaukan nauyin Karatunta ba sannan yarjejeniya ce akayi Mai zaman kanta,a Haka tana wannan rayuwar ta sake samun ciki cikin shekarar su ta biyu da Aure duk da bata so ba amma Haka nan Ta ɗauki dangana,
Duk wani wulakanci da take gani gidan Bilal dannesa tayi Ko yaya Abubakar bata faɗawa ba 'dan faɗan ma is pointless 'dan tasan babu mai duba mata kar  ma ace Daddy zaice kawai Zaman Auren ne bata so.

Hankalinta ta mayar kan karatunta wanda take samun nasarori sosai a ciki,gefe guda kuma tana kula da NADIYA yarinyar da ta shiga tsakaninta da BILAL Yar shekara,
Saukinta kawai NAMEER YARO DAN SHEKERA UKU a lokacin yana gurin Matar Yaya Abubakar "Sadiya" wadda ke nan cikin mansion d'in Bulama 'dan bai yarda Ko wanne ɗan sa Ya fita da iyalinsa daga gidan ba ,duba da gidane duniya guda.

CHUCHUJAY ✍🏾
To Be continued.
[10/21, 8:53 PM] CHUCHUJAY✍: AURE UKU

BY

CHUCHUJAY✍🏾

EPISODE2️⃣

Idan kana bibiyar labarin Rayuwar Umaimah zakace Shin dama masu kuɗi ma suna samun kalubale a rayuwarsu duk da kuɗinsu?

Zaka na tunanin tayaya Umaimah zata jure dukkan wannan Abun bayan mahaifinta sharararen Mai kuɗi ne!

Abun ba Haka yake ba,sau da dama kana da kuɗin da komai amma muddin Allah bai so ba baza ka ji daɗi ba tawani bangaren ,Ya 'dan ganta da kaddarar ka,

Auren dake tsakanin umaimah da bilal bai wani lasting ba saboda irin sharrin da suka haɗu suka haɗa mata,

Tana kwance kan Gadonta tana bacci ta tsinkayi hayaniyar mutane akanta,koda ta farka mijinta da mahaifiyarsa da matarsa ta gani a gefenta sai gefe guda wani ƙato da bata taba gani ba a rayuwarta kwance kan gadanta!

A ranar suka mata wulakancin da ta kasa mantawa a rayuwarta wato kazafun zina wanda ya Kai har bilal Ya ke tantamar kasancewar Nadiya yarsa ,duka bilal yayi mata sosai da belt wanda sai da Ya farfasa mata jiki kana ya sake ta saki biyu,

Abu na farko kenan da yaje kunnen Alhaji Bulama wanda yayi mutukar harzuƙashi,

Kuka sosai umaimah Take masa tana Mai masa rantsuwa akan bata taba Aikata zina ba hasalima ita bata san mutumin da ta farka ta gani a gefenta ba,

Mahaifin bilal Ya kira wanda baida masaniyar Mai ke faruwa saboda Ya rabu da mahaifiyar bilal,

Kwata kwata Alhaji bulama bai tsaya yi masa da sauƙi ba saboda yarda ranshi Ya baci,hakuri Alhaji muntari Ya bawa Daddy saboda shi bai masan wainar da ake toya wa ba,

Gudun kar zumuncinsu ya lalace yasa Alhaji Bulama yace masa zai bincike sannan yana so Ya fitar da hannunsa akan duk abinda zai biyo baya dan muddin Ya gane bilal ne baida gaskiya sai Ya ɗauresa.

DNA Ya fara sawa akayi conducting akan Nadiya da bilal wanda Ya fito 99% positive,

Da bincike yayi bincke aka gano haɗine na matar bilal da mahaifiyarsa ,baki ɗayansu Alhaji Bulama Ya daure a yayinda yasa a bawa bilal mugun kashi ladan dukan da yayi wa yarsa

sannan yamasa haramiyya da NADIYA.

Haka nan ta cigaba da zama a kano 'dan karasa karatunta wanda a lokacin tafi yinsa cikin kwanciyar hankali ,

A shekarar da ta gama karatunta ta haɗu da Hafiz matashin Mai arziki wanda haduwar farko Ya nuna mata soyayya ,ita macece da bata taba soyayyar ɗa namiji ba sai akan Hafiz ,

A hankali soyayya Ya kullo tsakaninsu inda baki daya bata ganin aibunsa musamman da yasan tana da yara biyu Ya amince da daukan su idan sukayi Aure ,

Da kalamai masu daɗi Hafiz yasa umaimah ta saki jiki dashi sosai,

Bayan ta gama karatunta ta samu licence na fara Aiki takai Hafiz gidansu a matsayin mijin da Take san Aure,

Kiranta Daddynta yayi Ya zaunar da ita Ya tambayeta akan gamsuwarta da Hafiz sannan Ya jaddada mata shi bazai sake ce mata ta Auri kowa ba idan tana so ma zata iya cewa bata so baki ɗaya bazai ce mata dan me ba,

Nuna masa tayi ta gamsu da hafiz wanda shima a hankali bayan binciken da yayi akansa Ya bada yardar sa akan Aurensu,

Da shagalin Aurenta da shagalin murnar samun aikinta Alhaji Bulama Ya haɗa mata gagarumun biki .

Kamar yarda Hafiz yayi mata Alƙawari kuwa Haka Ya ɗauki Nameer da Nadiya matsayin nashi,

Lagos suka wuce tare duba da yarda kasuwancin sa Ya tarkata chan,inda ita kuma ta fara aikinta cikin kwanciyar hankali.
Soyayya suke gwanin ban sha'awa a gidan Wadda tayi lasting na wata biyu kacal,

Hallayyarsa bata fara fito mata ba sai bayan dawowarsa daga wata tafiya da yayi zuwa indiya a lokacin da karamin cikin Abdallah ,babu kalamai masu daɗi Ko zama suyi hira mai sanyaya zuciya ballantana akai Ga mu'amala ta Auratayya,

Wasa Wasa tun abun tana ɗaukarsa wasa Har ya fara wuce tunanin ta,

Haka take dannewa tana koƙarin nuna masa kulawa amma hantara da kyara babu abunda baya mata.

A cikin gidansa akwai ɗaki guda wanda bata taba shigansa ba hasalima bata san dashi ba sai ranar da Yayi wata dawowa gida cikin dare a lokacin watan Abdallah biyu.

,tana jin shigowarsa ta tashi ta fito dan jin dalilin da yasa bai shigo da wuri ba,tayi mamakin ganin yarda Ya dana wani katon photoframe dinsa ,boyewa tayi ganin bangon Ya buɗe Ya bayyyana kofa,

Binsa tayi a baya a hankali ta shiga ɗakin itama,

Mamaki tasha sosai lokacin da ta ga wasu kayan tsubbu da pads na mata a jere a saman wani table,ba sai an faɗa mata ba tasan ɗakine na tsubbu,

Saurin komawa tayi da baya ta koma ɗaki jikinta na faman rawa musamman da taji yana faɗin zai kawo musu jarirai biyu kamar yarda yayi wa King manta Alƙawari.

Komawa tayi ta kwanta kamar tana bacci,

Dama bai kwana a ɗakinta a yanzu 'dan Haka ta saka key ta koma ta kwanta tana zulumi,Allah yasa Nannyn su NAMEER na tare dasu kuma suna kulle ɗaki,fargaba da tsoro sune kawai abunda Ke fama da ita,shekarar ta a lokacin Uku da Hafiz duk da fizge fizgensa bata taba sanin money ritual yake ba,juyawa tayi ta kalli jaririnta Abdallah tana ayyanawa kilan ma da Abdallah cikin jariran zai bada.

Tunanin barin da tayi farkon Aurensu tafra wanda tasha mutuƙar wahala duk da karamin cikine amma bata kawo komai ba musamman lokacin da ta tsincesa yana waya akan cikin wanda ya mata karya da Auntynsa ce.

Tafiyar gaggawa ta kirkira zuwa Adamawa wadda ko sanar mashi ba tayi ba,sallamar nannysu tayi ,a ranar da suka je adamawan da dare Ya kirata yana tambayar tana Ina ,karya ta masa tace taje kano ne karbo wasu takardu,sabida abin bai gabansa bai tambayeta abunda yasa ta tafi bata faɗa masa ba sai cewa yayi ta ɗauke Abdallah suje south Africa zai zo Ya samesu,

Batayi magana ba wanda dalilin hakan yasa shi buga mata wata uwar tsawa ,

To kawai tace masa ta kashe wayanta,

Bataje gidansu ba ,gidan kakanninta da Daddynta ya ƙera masu taje,

A ranar da safe ta tashi da labari Mai mutukar gigitarwa ,wai an kama Hafiz sannan ane neman iyalansa 'dan case ɗin da aka kamasu babba ne kuma mutum ɗaya daga cikinsu da hannun matarsa wanda Hakan yasa ake nemansu ,

Lokacin ta gane mai yake nufi da su tafi south Africa,

A ranar ta san wanda ta Aura,Ashe Hafiz babban ɗan yahoo ne wanda suke bada jinin mata da jirirai 'dan shi kam matansa biyu Ya bada umaimah ɗince yake ma san da bazai iya bada ta ba da ɗansa wanda dalilin hakan yasan asirinsu tonuwa,

Bai tsaya anan kaɗai ba harda safarar mutane wanda matar ɗaya daga cikinsu ke musu safara da yawancin yara da mata,ba ma nan kadai ba har Arm Robbery sunayi,

Tasha kuka sosai sosai lokacin da tagane wanda take so jabu ne,

He was lowkey 'dan duk binciken da mahaifinta yayi akansa bai gano wani nakasu nashi ba ,

Kawai an samu labarin shi ɗin marayane mara uwa da uba wanda Ahalinsa suka banzatar daga bisani kuma bayan wani Alhaji Ya jashi lagos yasashi kasuwancinsa wanda hakan ya habbakasa .

Ashe akasin Haka ne money ritualist ne,

Bayan zama da akayi a kotu da binciken da akayi akan umaimah aka yanke masu hunckin kisa ta hanyar rataya.

BAYAN SHEKARU BIYU.

CITY TEACHING HOSPITAL ADAMAWA STATE NIGERIA.

7:30 am

Cikin taƙama da kwarewa take takowa cikin harabar asibitin a yayin da wani Nurse ke riƙe da jakarta,

Idan akace maka tana da Yara uku zaka ƙara tsayawa ne ka Kalle ta da kyau har ka ƙaryata Mai faɗin maganar,

Asalin Umaimah irin matan nan ne wanda sukayi kyawu irin na fulani har zuwa jikinta, bata da ƙiba amma ba Haka ke nuna bata da ƙira ba,

Kirar jikinta ita ake kira kalangu,a fuskar ta babu abunda zai fara ɗaukar maka ido kamar sexy eyes ɗinta masu kama da tana jin bacci,

Zuwa Ga maidaidacin hancinta Mai 'dan tsayi sai cute lips ɗinta pink,

Ba tada yawaitar sakewa saboda irin abubuwan data fuskanta a rayuwarta ,kullum idan zaka ganta serious face ɗinnan ce kawai a fuskarta ,tsakaninta da colleagues ɗinta abunda Ya shafi aiki amma Babu alaƙa ta abota,mutane da dama akan gulmarta suke asibitin ,wasu suce girman kai ne ke ɗawainiya da ita 'dan tana ɗiyar Mai kuɗi wadda komai take so zata samu wanda sukance aikinma saboda shi ta samu saboda connection 'dan tana cikin manyan surgeons na asibitin.

Abun Ɗaya da basu sani ba shine da kuɗi nasiyan komai da batayi Aure uku ba,

A rayuwarta mutum ɗaya ta taba ƙawance da itama shekarar da take harvard suka haɗu HINDU duk da shareta da take bai hana HINDU tusa Kai rayuwar umaimah ba a yayin da ta sake mata duba da lokacin tana da ƙaracin damuwa 'dan rashin mahaifiyarta yayi ƙaranci saboda yarda mahaifinta ke nan nan da ita,

Kai tsaye Cabin ɗinta ta nufa 'dan Ko karyawa batayi ba,

Aje jakan nurse ɗin yayi kana yace"Dr Bulama,akan matar da za'ayiwa operation ɗin appendix ɗinnan yan uwanta sun saka hannu and kamar yarda kika faɗa yayi severe Dr Jabir yace Ya kamata ayi aikin da gaggawa 'dan shi yama sa hannu"

Dago Kai tayi ta kalli nurse ɗin tace"nurse farouk patient ɗina ne Ko na Dr Jabir mene Ya saka yasa min hannu?

Kara haɗe rai tayi tana Mai jin haushin yarda Dr Jabir ke mata katsalandan a aiki,

Shiru nurse ɗin yayi bai ce komai ba 'dan yana tsoran fadar abunda zai bata mata rai Cos she's short temper wani lokaci musamman gareshi wanda tunda tazo suke aiki tare,amma sau da dama shi zai fadi alkhairinta saboda tana masa,

Katse masa tunani tayi ta hanyar cewa"so ka tura mun detail ɗin patient ɗin,"?

Kaɗa kai yayi Kafun yace "yes doctor"

Jawo laptop ɗinta tayi tana faɗin "and I'm hungry jezzz!"

Juyawa yayi yana faɗin bari naje na kawo miki breakfast,
Saurin tafa hannu tayi alamun ya tsaya Kafun tayi saurin tashi tana cewa wait this is serious we Are going in for surgery now,

Yanzunnan akai ta OR yanzun nan and i need the team available ASAP.

Da sauri Nurse ɗin Ya fita ganin yarda ta fadin maganar ba Wasa.

Koda taje operation Room already team ɗin na nan,hannunta da tayi sanitizing ta miƙa aka samata Hand Gloves Guda biyu,kana ta juya aka sa mata rigan operation then aka ɗaura mata face mask.

Bayan gama operation ɗin cikin sa'a tana fitowa bayan tayi disposing Hand gloves ɗinta da face mask,ta juya zata tafi taji tayi gware da mutum papers ɗin hannunsa sun zube ,
Sorry kawai tace ta wuce ba tare da ta bawa wanda tayi gwaren da ba last kallo.

CHUCHUJAY ✍🏾
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU

(a hospital romance)

By

CHUCHUJAY.

EPISODE3️⃣

Kallo ya bita da shi a lokacin da ta rab'a ta gefansa ta wuce baƙinta da Kalmar Sorry wanda bayan nan Kallan Arziƙi daya bai ishe ta ba,

Tab'asa yaji anyi,

Dago wa yayi Ya kalli wanda Ya dafa shi ɗin Kafun yace "guy how far".

Murmushi guy ɗin yayi yace wa kake kallone Haka PAKI?

Yana mai tambayar nashi yana Kallan direction ɗin da yake kallo.

Dafe ƙirji PAKI yayi yace "Rayuwata nake kallo Kb,haƙarkarina da Ya bata na tsinta yanzun nan".

Dariya KB yasa sosai kafun yace "baka da lapia gaskiya ,ka bari sameera taji labari kaga wata kana faɗin kaga missing ribs ɗinka".

Tafiya PAKI Ya fara KB na biye dashi kafin yace"tun da nake da Kai tsakanin ka da Allah ka taba ji nace maka ina san sammy?"

Ita kaɗai take haukan ta wanda Ya kamata iyanzu kuma ku sani,

She's not My type of girl,i mean guy she's just not the one.

Kasan irin taste ɗin PAKI da na daɗe ina zayyana maka to yau na ganta cikin asibitin nan and insha Allahu sai ta zama ta IMAM MUKTAR PAKI.

Bai tsaya jin Abunda KB zai ce ba yayi gaba inda kb ɗin Ya bisa a bayan yana faɗin,guy hold on ana kiran mu 'fa Cos za'ayi attaching ɗin mu da snr doctors.

"To kawai yace masa suka nufi inda sauran young doctors ɗin suke".

Zazzaune suke cikin maɗaiɗaicin hall ɗin dake asibintin a yayin da Ko wannesu ke sanye da Farar lab coat,

Shigowarta ba karamun sa IMAM PAKI yayi ba cikin wani yanayi na shauki,

Bai taba jin irin Haka akan Ko wacce ƴa mace ba,zungurar sa KB yayi yace abokina kar kace mun itace,

Cikin wani irin yanayin farin ciki yace"Ya kagani ta haɗu Ko?"

Ƴar karamar dariya KB yayi yace baka da lapia,bafa cikin mu take ba mutumina likitace Mai zaman kanta,sannan ka Kalleta da kyau PAKI she's off limit,a fuska ma idan ka Kalleta kasan no nonsense ce,Kai kilan ma wallahi matar Aure ce.

Ba tare da Paki Ya ɗauke idanun sa akanta ba yace"KB jikina Ya bani ba matar Aure bace 'dan bazan taba jin yarda nake ji yanzu Haka akan matar Aure ba and da kake maganar she's off limit just look At me ,young and handsome ,sannan idan ita senior doctor ce nima Ai kasan

jan Kai ne tunda bana wasa da abunda Ya shafi Aiki ,beside saboda dedication ɗina first class holder ne wanda ba sai na faɗa maka ba,not to brag amma kai ma kasan idan magana ake ta ƴaƴan banki daga su nake,amma mutumina ba ta wannan ake ba batu ake na soyayyar ta da ta caccakar mun zuciya ,"Kai dai kawai idan mun gama abunda zamuyi anan muyi bincike akan ta 'dan Ko sunanta ban sani ba,

Ƙasa KB yayi da murya ganin Babban surgeon na asibitin Ya fara magana,yace"tana cikin hand book ni kam kamar naga hoton ta ,

And "..

Jan hannun sa Paki yayi yace "Kai yi shiru zata fara magana".

"Sunana Dr Umaimah Bulama ,surgeon ce da zaku yi aiki da,and ba sai na faɗa ba ,nasan dukkan wanda yake zaune anan yasan Abunda Ya kawo sa ,ba wai har kace ta Wasa ba saboda we are not some Artist or any sort of entertainers, we are here to save life da taimakon Allah wanda I'm sure shine aim na duk wanda ke zaune anan gurin ,idan kuma kana da wani otherwise aim to i will tell you that nan gun ba gurinka bane, So ba wasa just do abunda Ya kawoka,

If im right zaku ɗauki year a nan right?"

Yes ma!wani matashin saurayi Ya faɗa daga gefen su Imam,

Cigaba tayi da magana inda take cewa well,Ina muku fatan nasara a rayuwa And ina fatan zaku amafana da abunda zaku samu wanda za kuce gwanda da kukazo CITY HOSPITAL.

Bayan ta kai karshen maganarta gurin Ya ɗauki tafi ,a yayin da umaimah ta shiga kalbin young interns ɗin ,

Babu abunda Imam yake baya ga kallon ta yana Mai jin ta sake burge sa dan hatta muryarta wani abu take masa a kunne.

"Na shiga uku "Ya furta a hankali yarda KB kaɗai Ya jisa,shima ɗin maganar zuci ce ta fito fili,

Dariya karama KB yayi yace "Ai tukunna ma Alaji baka fara shiga uku ba."

Bai kula sa ba illa tasbihi da yake Ga ubangijin da Ya halliccesa Ya kuma halicci umaimah.

Bayan an gama ƙarbarsu aka rabasu ƙarkashin likitocin ,a Haka kaddara ta taka gudunmawarta wajen jefa Paki da KB karkashin Umaimah,

Sai wata yarinya Aisha shareef wadda ba ma makarantar su ɗaya da su Paki ba .

Fita tayi dan tana da VIP patients' da zata gani bayan ta wakilta Nurse farouk kan yayi addressing interns ɗin dake karkashin ta Kafun tazo and su tabbatar sun tsaya tazo.

Kallan KB imam yayi yace "kaji yin Allah ko?"Kai ni tunda na ganta nasan akwai wani boyayyen al'amarin da zai faru tsakanina da ita,
Gyara zama KB yayi yace wait paki mubar maganar wasa wai dagaske kake maganar kana santa?

Kalli 'fa ba tsararka bace,kar ka jama kan ka damuwa,

Dafa kafaɗar KB yayi yace "kwantar da hankalinka ,zaka maimaita maganar nan lokacin da kaga na sata a ɗakina ,kar ka manta Paki ne 'fa,wanda Ko wacce mace ta mutarwa a campus "

Suna wannan surutan Aisha shareef tazo yarinyar da aka sasu tare karkashin Umaimah,

Da fara'arta tazo garesu ,zama tayi kujerar dake kallansu tace"sunana Aisha Shareef,And zamuna aiki tare ne,

Washe mata haƙora KB yayi amma ita hankalinta yana kan Imam Paki wanda Ko inda take bai kalla ba dan yasan karshen maganar tace tana san shi. "

Miƙamata hannu KB yayi yace sunana"KABIR ASHIR abokina nan kuma IMAM PAKI,hope we will get along."Babu musu ta kama hannun KB tana Mai faɗan sunnan Paki a zuciyarta dan sunan Ya dace dashi sosai.

Bayan ta saki hannun KB ta juya ga Paki wanda hankalin sa ke kan waya ,hannunta ta miƙa

masa domin handshake,

Kallan hannun yayi sheƙeƙe kafin yace"last da na tuna ni dake ba muharramai bane sannan addinin musulunci bai yarda macen da ba maharramaka ba wani abu nata Ya ta b'a ka ,ban san wanne addini KB Ya shiga ba a yanzu da Ya kwakumi hannunki cikin nasa ,amma ni har yanzu ban fita ba ,bayan addini kuma I'm Allergic to handshakes cos it disgust me,"

Ganin yarda tayi da fuskarta gwanin ban tausayi sannan ta janye hannunta cikin sanyin gwiwa yasa Imam Paki cewa"hope zamuyi aiki Mai kyau tare".

Washe masa hakoranta tayi jin abunda yace ,cikin farin cikin tace insha Allahu,.

Bai sake ce mata komai ba Ya cigaba da danna wayansa inda yake jin suna hira su biyun kamar sun daɗe da sanin juna,

Tunda Ya duƙufa kan wayansa #tag DR Umaimah Bulama yake sawa yana san ganin duk wani post da Ya shafe ,da Haka ya samo profile ɗinta wanda ba komai sai abun da Ya danganci Aiki,

Har zai fita Ya ƙara komawa hashtag sunanta ,wani hoton ta ya gani a baƙin harvard university tayi murmushin daya bayyana well cleaned arranged white teeths ɗinta,

Gefe guda kuma wata kyakyawar mace ce da bazata wuce sa'arta ba ta dora hannunta kan kafaɗarta itama tana Mai mayar da murmushin,

Kana kallansu kasan suna cikin farin cikin irin na freshers da suka samu favorite course ɗinsu da suke ta mafarki,

Sunan Mai Account d'in da ta dora ɗin Ya shiga #HinduSD#

Scrolling Ya fara ,idanunsa ne suka sauka kan wani hoton Umaimah da yayi mutuƙar tafiya da imanin sa ,dimples ɗinta Ya lotsa sosai gwanin sha'awa ,

Hoton matric ne ,anyi tagging ɗinta ana wishing ɗinta happy birthday ,

Caption ɗin Ya duba yana san gani Ko ansa shekarunta,

#happy 25 baby,out of sight is never out of mind ,hindu forever Love you.

Irga shekarar da akayi posting ɗin yayi da yanzu yaga shekara Ashirin da Tara!

Duba Month ɗin da akayi posting ɗin yayi yaga birthday date ɗin 9th  march.

Dan leƙowa cikin wayar KB yayi yana san ganin me yakeyi bayan tashin Aisha ,karaf idanun sa suka nuna masa hoton Umaimah,dafa sa yayi yace guy Abeg Stop this.

Tsaki Paki yayi yace "rabu dani dan Allah ,nifa wallahi a yau kawai na kamu da san ta and guess what nigga"I'm 1 month older,wata ɗaya kawai na bata kuma bashi zai hanani cigaba da santa ba ,"

Ƙara dafasa KB yayi yace "Paki shekara ishirin da Tara 'fa ,taya kake tunanin bata da Aure ka rufa mana asiri,".

Tsaki yayi ya miƙe yace "sai kuma kayi tayi ai".

Sai wuraren shida na yamma umaimah ta nemesu,da rawar jiki Imam Ya ja KB sukaje cos duk yarda KB yaso su wuce sa haɗu gobe ƙi Paki yayi dan yana san sata cikin idanunsa .

A office ɗinta suka sameta,alamu ta musu da hannu akan su zauna,ta ɗauki lokaci tana danne danne a system ɗinta yayin da Imam ya ƙura mata ido yana Kallanta,

Bayan ta gama ta ture laptop ɗin ta kallesu tace"i guess mutum uku ne ya kuke ku biyu,And nace kujira ni".

KB ne Ya amsa mata ta hanyar faɗin"eh ɗayar Aisha shareef ce abun gaggawa yasa ta tafiya gida amma ta sanar da Nurse Farouk."

Kaɗa kai tayi tace "okay,"So

I guess kun san ni cos nayi introducing kaina earlier so names?

Kabir Ashir and Imam Muktar Paki.

Kallan Kb wanda Ya bata amsan tayi kafun ta kalli Paki wanda yayi saurin ɗauke kansa tace"

Wanene kurma a cikin ku?

Cikin rashin fahimta Kb yace na'am?

Dan karamun tsaki tayi tace "im sure mutum ɗaya bazai amfani da suna biyu ba,"

Cikin wata irin sassanyar murya Paki yace "im Sorry Dr"nine Imam muktar Paki"

Kallansa tayi na wani lokaci kafun ta ɗauke idanunta tace "so welcome to My team,i have less to say,first idan kana team ɗina sai ka shirya cos bana san wasa ,aiki aiki,idan kuma na fahimci mutum ba aikin yazo yi ba i will talk to the management Akai shi wani gurin cos im not in for rubbish, we have operation tomorrow By 9,"Mara lapian nada blood clot a brain so za'ayi masa Aiki gobe and we are going to the OR together,you may leave.

Har sun Kai bakin kofa tace "Paki"

Juyowa yayi yayin da gabansa yayi wani mumunan faɗuwa,

Nuna sa tayi da pen ɗinta tace"Ina fatan zaka rage kallo na and i just hope ba kallona kazo yi CITY HOSPITAL ba".

Dariya sosai KB Ya ke sheƙa masa lokacin da suka isa motar paki,

Dafa sa yayi yana kan dariyar yace "you fucked up Big time Paki,kaji haushi wallahi ,Bro control your self you don't even know this woman and daga gani Zatayi wulaƙanci she sounds Arrogant and wallahi Babu wuya Zatayi embarrassing naka,guy akwai mata da yawa Mai zakayi da tsohuwa she's 29 fa"

Wani banzan kallo paki ya bashi yace"with the attitudes na sake jin ta tafi dani and yes she's 29 and wata ɗaya na bata amma bakaji nace maka Ya dameni ba, beside she doesn't look her age Kai nifa koda ta girme ba zai dameni ba abu ɗaya Nasani shine INA SANTA,and wallahi idan ka cigaba da faɗan aibunta sai dai kana tafiya gida kai kaɗai har ka gyara motar ka "

Ɗaga hannu KB yayi yace "i rest My case".

CHUCHUJAY ✍🏾

Follow me.

Wattpad:@chuchujay

Instagram:ameenatourh__

Facebook:https://www.facebook.com/groups/805959663295457/?ref=share

Whatsapp group:https://chat.whatsapp.com/DgTUIodRcp2AHM4rmfKTqK

Telegram:https://t.me/chuchujaynovels

Join My telegram channel !

3 subscribers take me to 1000🤭

Arewabooks:https://arewabooks.com/book?id=653305e91c06f4783fc2ef84

To be continued.
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: https://chat.whatsapp.com/DgTUIodRcp2AHM4rmfKTqK

AURE UKU

(a hospital romance)

By

Chuchujay

Episode4️⃣

BULAMA MANSION.

8:00pm

Da blank tunani Umaimah taje gida,bayan tayi parking motarta ta nufi sashen da zai kaita bangaren Alhaji bulama,

"An dawo daga karuwancin da ake fakewa da aiki kenan a bar mana ƴaƴa ratate a gida da sunan anje aiki alhalin yawan banzan ne kawai ake zuwa,ki daiyyi zuciya kiyi Aure ,Ko da yake Auren fa bai ƙarbeta ba"

Muryar saleema matar yaya Aliyu autan hajiya zuwaira Ya daki kunnenta,

Da hajiyan da sadiya matar Ya Abubakar da Atika matar usman sai raliya matar Umar sai saleemar mata Aliyu,

Dukkansu suna zaune suna kallo a main palor wanda Hakan Ya tabbatar mata da yaran na tare da Daddynta,

Tun Kafun ta ƙarasa shigowa cikin ɗakin saleema tayi mata wannan raddin,

Takowa tayi bakinta da sallama ta zauna kan stool dake gefe guda ,

"Hajiya Ina wuni,sannu da gida"umaimah ta faɗa ba tare da damuwa ba amma tasa ar ranta yau sai ta mayar wa da saleema raddin da ta mata,

Ba tare da hajiya zuwaira ta ɗauke kanta daga Kallan da take ba tace lapia!.

Likita bokan turai an dawo kennan,

Sadiya ta faɗa wadda da ita kawai suke hirar Arziƙi sai wani lokacin raliya wadda bata cika sakewa da umaimah ɗin ba idan hajiya na nan,

Amma Atika kuwa jirgi ɗaya Ya kwaso su da saleema,

Murmushi umaimah tayi tace"wallahi yaya sadiya nasan su sultan ana chan ana damun Daddy,su Daddy Mai jikoki,"Gashi dai nawa uku,gurin yaya Abubakar Ga sultan ,sultana ga kuma Hameed ,gun yaya Usman ga ibi Ga rumaisah,

Gun yaya umar ma ga sayyid ga na ciki ,gurin yaya Aliyu ne dai ba motsi Ko sai yayi ta biyu kilan juya Ya samo bamu sani ba,tunda har yanzu ta kasa aje yaran ratata.

Ciƙe da balai saleema tace "uban wane Ya faɗa miki ana wa mutum gorin haihuwa,?"Hajiya kina jinta Ko ,gorin haihuwa 'fa take mun kuna jinta.

Tashi tsaye umaimah tayi tace"inji uban da yace kiyi mun gorin zaman Aure".

Bata jira jin mai hajiya take kokarin faɗa ba ta miƙe tayi ciki tana Mai faɗin gobe dan Allah idan kin ganni ki sake sakar bakin ki da bashi da gashi,nonsense.

Koda ta haɗo kan yaranta ta kofar baya suka bi 'dan bama tasan abunda zai sake haɗa su,

Zama tayi kan kujera Abdallah na kan cinyarta yana ta zuba mata surutun sa wanda galibi hirar Adda diya ne, kallan nadiya dake fama tutura baki tayi tace "lapia diya kike ta faman turo baki "

Kuka tasa kamar tana jira tace"wallahi mami ni gidan Dada (kakar umaimah)zani na gaji da zaman gidan nan ,kullum cikin cin zalina hamma NAMEER yake yana kuma Kallan yarda hamma sultan ke ji da Adda sultana da hameed,amma ni ina yin abu zai buge ni ,kowa a gidan nan haka suke mun hamma sultan ne kawai bai mun Faɗa nidai mami nagaji,"Haka jiya hajiya ma cemun tayi wai ni da hamma NAMEER da Abdallah baban mu ba ɗaya ba kuma wai baban Abdallah barawone ɗan shan jini,

Koma mami ba yau ta fara faɗa ba ni bana so .

Wani iri umaimah taji a zuciyarta jin abunda nadiya ta faɗa ,dole zata ma tufkar hanci 'dan bazai taba iyuwa ba ace ana faɗawa yaran ta magana irin wannan.

NAMEER '

Ta kwalawa nameer wanda Ya wuce ɗaki kira tayi dan yasan dama nadiya sai ta kai ƙkararsa .

Na'am mami'

Ya faɗa yana Mai fitowa falan,

Zama yayi yana faman zare ido,

Kwantar da muryarta tayi cikin murya wadda uwa ke koƙarin jan ɗanta a jiki tace""Nameer Mai yasa kake dukan nadiya?

Mai yasa ba kasan na zauna lapia When kaine babba amma kaine ka kasa jan kannen ka a jiki

,kana so kace mun idan Abdallah ya Kai duka shima zaka dake shi Ko?

Haba nameer why Are doing this to your mother you're 11 years old for GOD sakes,

Dawowa tayi kasan da yake zaune ta zauna ta jawo hannun sa tace "nameer ka ma mamin ka magana maine yake damuka?"Why Are you always this bitter.

Kuka Ya fashe dashi yace "mami i dont like this house ,mami kamar yarda diya ta faɗa maki yan gidan nan basu da aiki sai faɗa mana mamin mu ta haife mu da baba daban sannan wai baki da time ɗinmu,and mami its frustrating da yasa nake venting anger na kan Nadiya,  "Riƙe hannun umaimah yayi yace "mami 'dan Allah mubar gidan nan im sick of it"

And wai mami ibi har a class yake faɗan wai mamin mu na da miji da yawa and the kid's are always tease me,

wallahi mami saboda ke nake dagawa ibi kafa da tuni na daɗe da karya masa hannu,sai dai Uncle usman ya kasheni 'dan ranar ma 'dan ibi Ya tsokane ni na rama Ya buge ni.

Wani irin zafi taji a ranta ,jawo sa jikin ta tayi ,kana tayiwa nadiya ma alamun tazo ,shafa kan nameer tayi tace "nameer what matters is na haife ku,"Menene 'dan baku sharing DAD ɗaya ku uku?

Yes kai da Nadiya da Abdallah daddynku daban Cos kaddaran mamin ku shine Aure guda uku har ta sameku wanda rabon ku yasa ,sannan ina farin ciki sosai da Allah ya bani ku,

Duka wannan doesn't matter  ,abu ɗayane wanda zaku sa a ranku, maman ku ɗaya,ni maminku and Nothing is gonna Change that,sannan maganar bani da time dinku shima kunsan Ai ba gaske bane,i celebrate each of your birthday's tare and we had funs ,muna zuwa park tare wani ma maminsa na tare dasu amma basu samin wannan damar .

I promise you guys babu mai sake teasing ɗinku a gidan nan,and duk wanda yayi muku a school just tell them that"you have a strong mom that love you."

Abu ɗaya zaku mun shine ku tsaya ga junan ku like one big Family,im here ,nameer ,nadiya and Abdallah ,tafun hannunta ta buɗa tace team?

A tare dukkanin su suka washe baki ,nameer ne Ya fara dora hannunsa kan na umaimah Kafun nadiya tasa then 3 years old Abdallah da shima yayi abunda sukayi yana dariya.

Washe gari da kanta tayi dropping ɗinsu a school ba ta yarda sun bi school bus ɗin su na gida ba 'dan ta shirya,she's going to create havoc,

Sanin suna da theater yasata shiga asibitin da wuri 'dan su shirya,

Tana kokarin parking motarta taga baƙuwar mota a gurin,

Da mamaki ta fito tana san taga uban da yayi parking motan sa gurin da take aje tata 'dan koma wane zai ƙarbi peace of mind ɗinta dan a zafinta tazo,

Security ɗin dake gun ne Ya tako da saurinsa ganin bata paka motan nata ba,yana Mai girmamata yace"hajiya lapia dai ko" .

Ƙaramun tsaki tayi tace"lapia ce zata sa ka ganni ban parking mota ta ba na shiga cikin asibiti bayan Ina da abunyi Mai amfani maimaƙon tsayawa maida zance da kai?

Uban wanene Ya faka motarsa a inda nake aje tawa ? "

Daga jin furucin ta yasan cewa tabbas akwai wanda Ya tab'a jar danjar ta ,'dan in dai dama kaji ta shigo tana faɗa to da damuwa ta shigo tana neman wanda zata saukewa 'dan haka ba tare da Ya damu da abunda tace ba yace"hajiya ga chan gefan kinga ba mota mai zai hana ki sa taki gun".

Kamar tana jira tace"Kai bazan Aje ba,nace maka bazan aje ba Ko zaka mun dole ne?"

Nurse faruk da ƙarasowarsa kenan ne Ya tako gun yana faɗin lapia?

Kamar shima tana jiran sa tace ,lafia ne zaka ganni anan?

Abeg aje a nemo mai motan nan yazo ya ɗauke gwangwanin sa i don't have time to waste,

Kallan range rover ɗin da ta kira da gwangwani Nurse farouk yayi a ransa yace"lallai yau uwar ɗakin sa da fushi tazo".

Cikin takun nan dake burge Yan mata Imam Paki ke Takowa inda umaimah suke,KB yaje ya bashi latest ɗin abunda umaimah keyi a waje,

Tunda ya matso daf dasu yake wani irin murmushi Mai ƙayatarwa wanda umaimah tunda ta hangosa Take jin kamar tayi wiping wannan murmushin dake manne a fuskarsa ,

Motarsa ya shiga Kai tsaye Ya gyara parking a ɗayan gefan da akace tayi parking tata taƙi,

Kamar tashin hankali Haka ta shigar da tata motar,

Shi Ya fara fitowa Ya nufi motar tata ,tana koƙarin buɗe kofar yaje bakin kofar Ya tsaya ,

Ɗago Kai tayi ta kalle sa tace "Ina fatan kwakwalwarka bata samu matsala ba?"Ko wait ,kasha wani abune Kafun kazo nan?

Ƙasa yayi da muryar sa yarda ita kaɗai zataji abunda yake cewa yace"eh nasha giya ce ta soyayya ,ita ke ɗawainiya dani"

Murmushi yayi Mai kyau kana yace"a yin fushi ma Kin hadu DR babu wanda ya tab'a faɗa miki Haka? ".

Ɗaure mata Kai abun yayi sosai dan bata san inda maganganun nasa suka dosa ba ,Zatayi magana cikin fushin da ta kwaso daga gida Ya ɗora hannunsa kan lips dinsa yace"shhh its not Good for your health and kar ki manta doctor jiya da kakkausar murya kika ce mana akwai aiki ,ban san dalilin da ya saka fushi a wannan fuskar taki Mai tsada ba ,amma inaso for now ki cire an jima sai a cigaba Ko Mai kikace ?

Ya ƙarasa yana Mai ɗaga mata gira ".

Saurin matsawa yayi a bakin kofar Ya kama hanya da sauri ganin abunda Ya gano na masifa idanun umaimah,

Yanzu Ya shirya kuma bazai fasa bayyana mata soyayyarsa ba koda kuwa kullum zata na zaginsa ne.

Tafi minti 30 tana zaune a inda ya barta ,

The guts kawai take Maimaitawa a zuciyar ta,lallai dole ta taka ma yaran nan birki cikin asibitin nan dan taga alama bashi da kunya.

Dr Bulama saura 50 minutes a shiga surgery ɗinnan and you need to get ready ,ina fatan lapia dai Ko?

Nurse farouk Ya faɗa 'dan gajiyar da yayi da tsayuwa.

Wani irin kallo ta bashi Kafun ta fito a motan tana Mai cilla masa key dinta tace "kasan Mai zakayi".

Ƙada kai yayi Ya ɗauko jakarta da wayanta yabita yana Mai tsinewa wanda Ya tab'o Dr bulama,

Tana shiga cikin asibitin taji Dr Jabir yana faɗin"The mighty snr surgeon ina fatan Kin shirya faɗuwa a operation ɗin da zakiyi yau tunda naga tunda kika fara ba'a mutu ba amma Ina san ki sani wannan karan 2% chance of living patient ɗin keda ,idan zaki cire girman Kai ki bani aikin nan then na tabbatar miki it will be a success ".

Juyowa tayi ciki takalminta mai tsini ta taka garesa ,ganin zata haɗe dashine yasa shi ja baya a yayin da ta bisa har sai da ya Kai maƙura,nuna masa dogon yatsanta tayi tace "da fari idan

baka fita harka ta ba zan wulaƙantaka a asibitin nan,idan kuma kana ja dani ne Dr jabir mu zuba ni da kai.

Kar kamanta nace bana sanka wanda nasan shi yasa kake shigemun saboda baƙin ciki, na manta ban faɗa maka tun ranar da ka fara cewa kana sona na so na faɗ maka kana buƙatar dentist dan kana da disgusting mouth odour "sadly im not a dentist,

Snapping Hannayenta biyu tayi tace ka kula.

Ta juya zata tafi kenan ta tsinci muryarsa yana faɗin,dama Mai zanyi da beljiun ,second hand ,Ko kina tunanin bamu san Aurenki Uku ba har da yara Uku,

Duk kuɗin babanki da sanayyarsa a ƙasa da ketare Ya kasa zaunar dake ,ko kina tunanin bamusan rabawa matan manyar kasarnan jikinki ne ke hanaki zama guri ɗaya ba.....

Follow me on wattpad :chuchujay

Arewabook:https://arewabooks.com/book?id=653305e91c06f4783fc2ef84

IG:Ameenatourh__

Facebook:https://www.facebook.com/groups/805959663295457/?ref=share

Chuchujay ✍🏽

To be continued .
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: https://chat.whatsapp.com/DgTUIodRcp2AHM4rmfKTqK
AURE UKU

(a hospital romance)

BY

CHUCHUJAY

EPISODE5️⃣

Riƙe Paki dake koƙarin yin gurin KB yayi gam yace"no Paki ,no wannan maganar ba wadda zaka shiga bace ,damƙe hannu Paki yayi kamar zai kaiwa wani naushi yana Mai Cije haƙoran sa, yasan da fushin da tabbas idan Ya je gurin zai zubarwa da Dr Jabir haƙora ".

Juyowa umaimah tayi a lokacin da maganar Dr Jabeer ta dakar mata zuciya dai dai saitin da yake mata ciwo,

Ta daɗe tana jin rumours ana cewa tana rabawa matan masu kuɗi irin su jikin ta shi yake hana ta Aure, amma bata taba samun wanda Ya faɗa mata kan fuskarta ba,

Bawai abun baya damun ta bane, yana damun ta musamman yarda jita jita ke cigaba da yaɗuwa akan ta,

Shin wai ita ta ɗorawa kanta ƙaddarar da Allah Ya jarabceta da?.

Ɗan karamun murmushi tayi tace "za kaga ƙarfin connection,ba kace kuɗin babana bai zaunar dani gidan Aure ba?"Zaka Ga yarda yarda kuɗin babana zai daure ka for defamation of character tunda baka taba ganin lokacin da na bawa Ko wacce mace jikina ba kamar yarda ka faɗa,

I'm gonna show you what money can do here Jabir,

If you'll excuse me.

Juyawa tayi tana mai Jin wata kwalla na zubo mata wadda tayi saurin gogewa a lokacin guda kuma idanun ta suka sauka kan Paki wanda ke tsaye yana Kallan abunda ke faruwa ransa a mutuƙar bace kar ma ace Da Ya lura da kwallar cikin idanunta.

Ɗauke idanunta tayi daga nashin ta nufi cabin ɗinta 'dan shirin Aikin da za tayi,

Gama shirinta ke da wuya ta juya zata fito taga an buɗe kofar,ɗagowa tayi,

Idanunta ne suka shiga cikin nasa,

Cire idanunta tayi cikin nasa tana Mai kashe wayanta ,

Muryarsa ta tsinta a yayin da yake faɗin,"zaki iya yin Aiki a haka".?

Wata irin karamar dariya tayi ta ɗago da idanunta ta kallesa tace"first this is My personal cabin 'dan na tabbata a sama Kafun ka shigo kaga an saka Doctor Bulama's Cabin Nasan atleast ka iya karatu zuwa nan,

Secondly we Are not that close beside ban san ka ba,ina so ka riƙe wannan Alaƙar ta supervisor da dalibi itace tsakanina da kai dan naga alama kana san wuce gona da iri,kasan limit ɗinka,

Thirdly ina san ka sani,i dont mix duk wani abu da Ya shafi Aikina da wani abun duk girmansa so don't mistake what happened as My weakness

Now get out."

Gyara tsayuwar sa yayi yana Mai folding hannunsa a kirjinsa cikin blue kayan likitoci, a bangare ɗaya kuma yana mata wani irin kallo Mai kashe jiki,

Coffee ɗin da ya kawo mata Ya aje kan table Ɗinta har lokacin idanun sa na kan idanunta Kafun yace"cold coffee ne 'dan nasan ba lallai kin karya ba,a lokutan da kika ware na Aikin da za'ayi kinci minti goma a waje ,komai yayi ready ke ake jira ,so take the coffee and ina san ki sani Ko Auren ki goma a duniya da yara kimanin faɗin duniya akwai wanda hakan bai dame sa ba da

duk wani Abu da za'a faɗa akan ki.

Juyawa yayi Ya fita a cabin Ɗin.

Bin kofar tayi da kallo a yayin da taji cikin ta yayi wani ƙugin yunwa,

Daga cup Ɗin coffee ɗin tayi ta shanye Cos bata san shiga O'R ba tare da tasa komai a cikinta ba,

Amma tabbas za suyi magana dole tasa gayen nan a inda ya dace dashi.

****

Kamar kullum yau ma bayan tayi sanitizing hannunta ta shiga operation room ɗin da hannunta a ware tana tsoran kar wani infected abun Ya tab'a ,dukkan team ɗinta sun hallara tare da IT student Ɗinta guda uku,

Bayan ta zama set ta koma kan mara lafiyan da batama san duniyar da take ciki ba tace "hour nawa aikin nan zai dauka Dr Fatima?"

1 hours doctor "Dr fatima jnr ɗin umaimah ta faɗa professionally,"

Timer ɗin da akayi setting ta maida minti 40  wanda Ya bawa interns ɗinta mamaki karma ace Paki,

Daga gefen su Aisha shareef tayi murmushi a hankali tace"i admired her naji ance she's the most fastest doctor here".

Cike da kwarewa tace"zamu gama cikin 30 min And kamar yarda kowa yayi reading its not just hematoma But subdural Hematoma And the patient have 2% chance so Ya 'dan ganta da luck dinta But we would do our very best,

A hankali ta fara neman larger access to blood clot ɗin,wanda shine (craniotomy),

Inda ta cire section na ƙashin dake tare mata hanyar gudan jinin,

Bayan ta kammala,ta replacing section na ƙashin kafun ta rufe soft tissues ɗin ta hanyar amfani da sutures .

Maida hankalinta tayi kansu Paki tace "warkewar mara lafiyan kuma zamu barwa Allah ne but the operation is done and its a success ,And since nayi undergoing craniotomy warkewar zata dauki lokaci ,so yanzu za akai patient ɗin recovery room Kafun a kaita ICU once situation ɗin is stable she would be moved to the regular room har a sallameta,duk Mai tambaya Ya bini office, so nayi highlighting ɗinsa "Alamu tayiwa sauran doctors da nurses ɗin kan su dauka daga inda ta tsaya Kafun ta fita,

Idanun Paki ne Ya sauka kan timer wanda sai yanzu ma yayi clicking 50 min,

Faɗa yayi da bakinsa,

Murmushi Dr Fatima tayi tace "she's the most fastest doctor da zaku gani a asibitin nan ,idan kuka maida hankali zaku karu da ita sosai.

Kallansa Kb yayi bayan sun fita yace mutumina zo muje mu zanta mana.

Babu musu Ya bishi duk da yana san zuwa gurin umaimah da excuse ɗin yana da tambaya,

Kallan KB yayi bayan sun zauna yace"Paki kasan dai ni da Kai mun wuce abokai sai dai yan uwa ko?

Ni da kai tare muka girma mun damu da damuwar juna da duk wani abu da zai zamar mana Mai kyau,

Kalli nan Paki sameera yarinyace Mai kirki duk da nasan wani lokacin tana da rawar kai amma na yarda da san da take maka kuma zaka iya juyata duk yarda kake so amma mutumina kai kanka kasan maganar Dr umaimah ba abune Mai iyuwa ba ,kai kasani Ko kowa Ya amince Nana bazata taba yarda ba,

Kai babu ma wanda zai taba Amince maka da maganar ta kaima ka sani,

My guy Auren ta uku 'fa har da yara Uku,kasan maine Ya fito da ita daga gidan mijinta?

Baka taba Aure bafa tayaya kake san duniya ta fara ɗaukar maganar nan?

Bro ni nafi tunanin ma harda attitudes Ɗinta ya fito da ita gidan mazajen 'dan tana jin babanta Attajirine ,i mean guy she's rude with words,

Na yarda rumours ɗin dake yawo akanta jitajita ne amma kasan gaskiyar ne?.

Dan Allah imam ka sake wani tunanin amma hanyar nan da ka ɗauko mana ba mai bullewa

bace kwata kwata ,

"Bayan Ya shigo ya tsaya a tsaye yace"Dr Bulama Kin kirani and Na tsaya stitching  ma wani patient ciwo ne as per Nurse Farouk instruction".

"Kallan sa tayi da kyau jin yarda yake mata magana kamar bashi ba, "

Alamu ta masa da hannu tace "zauna"

Cike da kafewa yace"im okay Dr and Dr Kaseem yana nemana idan babu damuwa ina san ki faɗa da sauri,idan ba urgent bane kuma naje na dawo".

"Cikin sosowar rai tace Imam paki have a seat bana san na sake repeating kaina, "

Kamar bazai zauna ba amma sai Ya zauna ɗin yana Mai Kallan gefe.

Ji tayi wani irin yanayi na rashin dadi Ya ziyarceta,

Cikin kulawar da bata san tana da ita ba tace "akwai abinda ke damunka ne,"Zan ma Farouk magana Ya dubaka.

Murmushi yayi kafin yace "a makarantar mu nine must brightest student,sannan na fita da First class, bangaren medicine kenan kama ai kinsan ba abun Wasa bane,so ina da capability ɗin ganewa idan bani da lapia ko a'a bana buƙatar kowa.  "

"Haka nan taji yayi mata wani irin kwarjini a karo na farko,"

Dan har tana hada in ina a maganarta musamman yarda taga Ya kuramata ido da wani irin yanayi,

Sauke idanun ta tayi saboda yarda taji Idanunsa na mata a cikin nata.

"Wani irin murmushi yayi yace"Dr Bulama Stop making me feel less,i can fight for me,ni namijine da yasan right ɗin sa,im not some coward ,and yes im not scared 'dan nace ina sanki cikin gurin Chan mai cike da mutanen banza ".

Ai ba laifi nayi ba ko sab'awa mahalicci ,ina sanki kuma har gobe ina sanki, and nasan kinajin wani abu a zuciyarki a tatare dani,

Musamman idan ina tare dake ,idan kikaji muryata nasan zuciyarki na bugawa da sauri,

Sannan idan baki jini ba nasan kina kewata.

Amma Zan ɗaga miki kafa tunda kamar ina zaƙewa da yawa,duk lokacin da kika gama tattara shawararki akaina ni a kullum ina tare dake ,sannan maganata da nafaɗa na barin field ɗin nan idan har bakiji wani abu na soyayyata a tatare dake ba nan da shekarar da Zan bar nan then na maki Alƙawari zan aje mafarkin zama surgeon .

"Yana gama maganar sa Ya tashi yakama Hanyar fita ,yana ji tana masifar Ya dawo bata gama dashi ba and how dare he zaina Wasa da mafarkin sa akan soyayya."

Banza Yayi mata,tun ranar Ya chanza Mata baki ɗaya ,tun tana wa kanta excuse akan baya damunta har zuciyarta ta yi ƙarfi wajen karyata ta 'dan sosai take jin abun har ranta ,musamman a yanzu da taga wani kusanci da Ya shiga tsakanin sa da Aisha shareef musamman idan tana musu lecture.

*

Cikin sati biyun nan halayyar paki ba karamin damunta take ba,cos a yanzu tunanin sa yana ɗaya daga cikin abunda yake hanata sukuni,

Kafun Hindu ta wuce tasha faɗa mata tana san paki ne wanda take shan mur tace Ai karyane ita ba sanshi take ba amma a yanzu tana neman ta ƙaryata kanta.

"Kai tsaye bayan Ta raka su Nameer Airport tayo asibitin,

Tunda ta shiga take san ta sa idanunta akan Paki amma bashi babu alamun sa,

A ranar koda taga babu shi bata tsaya basu wani lecture ɗin kirki ba,

Bayan ta gama suna fita,tace "Kabir ashir."

Juyowa yayi yayin da ta masa alamu da hannu akan yazo,

Babu musu yaje yana Mai boye karamin murmushi a zuciyar sa yana faɗin "shege paki yasan Mai yataka.

"Kamar kuwa yarda yayi expecting yana zuwa tace paki 'fa".

"Dan Sosa kai yayi yana san tuno yarda Paki Ya shirya masa kafin yace"Ai Dr Paki yana gida bashi da lapia sosai,"

"Cikin reaction ɗin da bata san tayi ba tace "bashi da lapia kuma?"

Mene yake damunsa?

And idan baya da lapia mai yake a gida?

Boye dariyar sa yayi yace"Ai yana Chan kuma rashin lafiyar sosai yake amma ko ummu bata sani ba 'dan yana part ɗinsa a kunshe".

Cikin damuwa tace "and kake nan Kana faɗa mun when Kana abokinsa,idan shi baya san lafiyansa Ai akwai masu so".

"Na'am ?"KB ya tambaya bayan sarai yaji abunda tace,

Wani irin kallo ta bashi musamman da ta fahimci abunda tace,

Tashi tsaye tayi tace ,

"Kaini Gidansu."

*********

So jiya baku samu update ba cos banji daɗi ba ,

But im Good.

To munje gidan Muntari ɗan Nana Mai abun mamaki,

Team# pakiumaimah

Kuna kusa?

Chuchujay ✍🏽

To be continued .
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: https://chat.whatsapp.com/DgTUIodRcp2AHM4rmfKTqK
AURE UKU

(a hospital romance)

By

Chuchujay✍🏽

Episode 1️⃣7️⃣➡️1️⃣8️⃣

Tsaye taki bakin katafaren mansion ɗin su Paki tana tunanin abun da ya kawo ta ba tare da tayi tunani na biyu ba,

"Wata zuciyar na faɗa mata ta koma saboda bata san abunda zata ce ba idan ta shiga,tunda dole tasan yana tare da iyayen sa,"

"Wata zuciyar kuma tace mata "taje a matsayin Caring doctor ɗin da yake ƙarkashin ta After all babu wanda yasan baya da lafia ɗin,"

Kallan Kb dake kallan ta tayi tace lapia?

Murmushi yayi yace "lapia kalau Dr ,ina so ne kawai na faɗa miki,Paki yana mutuwar san ki,sannan saboda Allah yake sanki,tunda nake dashi babu ɗiya macen da Ya tab'a nuna soyayyar ta ƙarara kamar taki,".

"Kallan sa tayi Kafun ta ɗauke idanun ta kamar abin bai affecting ɗin ta ba tace "zaka mana jagora ne ko kuma na shiga da tambaya".

Faɗaɗa fara'arsa yayi a lokacin da Ya jiyo humour cikin maganar ta,

Baisan tana da wannan side ɗin ba.

Kafun yace "cikin da tafiya yi horn sai mu shiga."

Gate biyu ne a gidan wanda tsakanin gate na farko dana biyu akwai yar tazara,tun daga gate ɗin farko tasan Paki yaran Soldier ne ,taso tayi sensing a case ɗin su Dr Jabir ganin yarda sojojin ke basa ladabi.

"Sojoji ke gadin su dan sune gate ɗin farko dana biyun,"

Ganin KB ne yasa basu tsare su ba suka basu damar shiga,

Ba tare da ta kalli KB ba tace "dad ɗin paki hala soja ne?"

Kaɗa kai yayi yace admiral ne ,yaso sosai paki yayi aikin amma yaki wanda nafi maidashi ga kaddarar haɗuwa dake takaisa Likitanci.

Tsintar kanta tayi da yin murmushi wanda bai kub'ucewa KB ba,at least yanzu hankalin sa Ya kwanta daya gane Abokin sa ba haukan banza kawai yake ba.

"A gefen expensive motocin gidan ta faka tata,"

KB ne Ya fara fitowa Kafun ita,

Haka nan taji gabanta na faɗuwa,

Kallan Kb tayi tace "is it okay.

Kaɗa mata kai yayi Kafun Ya fara tafiya tana binsa a gefe,

A bakin wata wide kofa dake rufe suka tsaya inda Kb Ya danna door bell,

Minti ƙalilan aka buɗe kofar,

Sameer ce tsaye "idanun ta na sauka umaimah ta haɗe rai kamar an aiko mata da saƙon mutuwa tace"uban me Ya kawoki nan?

Kin biyo sa gida ne a cigaba daga inda aka tsaya tunda ke roban pants ɗinki ya sake baya Kama miki ƙugu. "

KB na koƙarin magana muryan ummu da ta Aiko ta ta buɗe ta katse ta a yayin da take cewa""Ke Sameer wa kike faɗawa maganar rashin ɗa'a haka.

Faɗada murmushi umaimah tayi Nervously a lokacin da Ummu ta bayyana wadda ke mutuƙar Kama da Iman paki,kana kallanta kasan mahaifiyar sa ce,

"Matsa mun bakin hanya nan,Au kabir kune ma ,Kallan umaimah tayi Kafun tace "da ita kike,"Baiwar Allah kiyi hakuri dan Allah ku shigo daga ciki,

Kiyi hakuri.

Murmushi umaimah tayi ba dan maganar sameera bata mata zafi ba,ita bama tasan sameera gidan take zaune ba da ba lallai tazo ba dan ta fahimci yarinyar notinan kanta a kunce suke.

"ƙara gyara fara'arta tayi tace "babu komai Ummu,

Shiga ciki tayi ga jagorancin Ummu wadda ke daɗa bawa umaimah haƙuri tana maiwa Sameera Faɗan abunda tace mata .

Zama tayi cikin ladabi ta gaidata kafun tace "sunana Dr Umaimah Bulama ,sannan nazo ne dan duba imam paki ,muna tare  ne a asibiti so naga yau bai zo ba Shine kabir ke sanar dani bashi da Lafiya and its severe sannan bai sanar da kowa ba.

So nazo ne naga Ya jikin nasa".

Daga gefe sameera tace "da bashi da lafiya Ai mu zamu fara sani ba ke ba ,kawai dai kice da abunda ya kawo ki".

"Wai nikam sameera zaman Mai kike anan?"Bana san shashanci da iya shege 'fa,maza tashi

kibar nan,

Ummu ta fada cikin jin sameerah na sake sire mata,

Da zumbura baki ta tashi tayi sashen Paki dan san gano gaskiyar Umaimah.

Dan kallanta ummu tayi tace "Umaimah,kece wadda wannan abu mara daɗin Ya faru tsakaninki da Imamu na ko"?

Ɗan kasa da kai umaimah tayi tana Mai jin kunyar Ummu kafun tace nice".

"Allahu Akbar ,Allah sarki,abun baiyyi daɗi ba,and naji daɗi da aka kamo waɗanda sukayi cos tunda abun nan Ya faru da Imamu na dai ,amma zuciya ta tana gare ki,

Sannu ko."

Murmushi umaimah tayi tana Mai jin kaunar ummu kafin tace "ai ummu dama mutum baya cika idan baya samun jarabawa".

Kaɗa kai ummu tayi tana Mai faɗaɗa fara'arta tace "hakane ƴata,Allah Ya bamu ikon cinye dukkan jarabawar rayuwar mu,"

"Kai kuma Kabir kace Imam bashi da lafiya?

Inace gidan nan ka kwana Ya akayi baka sanar dani ba tun ɗazu yana ɗaki akwance idan da karar kwana kuma 'fa.

Ɗan Sosa kansa yayi yana Jin nauyin yiwa ummu karya kafin yace"Ai ummu da na fita na barshi yasha magani ma Shine yace kar na faɗa miki cos zuwa jimawa ma zaije asibiti so daga baya kuma ya kirani,"Zan taho gida ne Dr Umaimah ke tambayata shi ,Shine na sanar mata.

Kaɗa kai ummu tayi tace Amma dai kun cika shiririta,

Bari naje na gani ,

Tashi tayi ta nufi hanyar sashen Su pakin,

Bakin kofar ta tarar da sameera tana ta aikin kwankwasa masa kofa tana cewa yazo Ya buɗe mata,

"Lapia dai ko?"

Cikin kiɗimewa tace ummu Ai ya mutu a ciki ,inata bugawa ko alamar sa banaji.

Tsaki ummu tayi tace "matsa mun dan Allah,ke kike shiga kika kashe shi ai"

Knocking tayi tace "imam open this door ,"

Yana jin muryar ummu Ya taso Ya buɗe kamar mara lafiyan gaske yace ummu?

Da gudu sameera ta shiga gaban ummu tana Mai kamo hannun sa cikin wata irin murya tace "wallahi na zata ka mutu a ɗakin nan har hankalina Ya ɗugunzuma Ya tashi sosai ".

Jawota ummu tayi ta mayar gefe kana ta kallesa daga sama zuwa ƙasa ,hannun ta tasa gefen fuskar sa ,cike da kulawa tace "Imam lafiyarka ,"

"Mini Mini yayi da idanu yace"Ummu im sick,"

Cikin kulawa ta Kama hannun sa ta shiga dashi kerarren ɗakin sa ta zaunar dashi kan kingsized bed ɗin sa dake yane da ash bedding ɗin da ba'a gyara ba tace "amma imam mai yasa baka kirani ba ? "

"Nima Ummu da Ya kirani zanzo ba sai Ya ƙira wacchan balagazar matar ba."

"Dan rintse ido ummu tayi kafun tace"sameera kije ko,"Zan magana da imam ne,

"Tsayawa tayi tace amma ummu.."

Kafun ta ƙara cewa wani abun ummu tace "nace kije ."

Da turo baki ta fita a ɗakin.

"Sarai yasan wa sameera ke nufi amma gudun kar ummu ta rafkosa yasa shi langwabewa yace "ummu wacece tazo?"

Murmushi tayi tace"Dr Umaimah ce tazo duba jikin ka,ban san tana da kirki haka ba, naji daɗin zuwan nata,

Tana da ladabi sosai,ina santa".

Wani irin daɗi yaji aran sa kafun yace,"yauwa ,ummu tazo ta dubani ,dan ko asibitin naje gurin ta zanje cos ita kaɗai tasan abinda yake damuna.

Cikin rashin Fahintar inda Ya dosa ummu tace"to ka zo muje babban falo tana Chan sai taga jikin naka ,"Ko tazo nan?.

Kara langwabewa yayi yace ummu tazo nan kafafuna ji nake kamar bazasu ɗauke ni ba.

Tashi tayi tana cewa "shikenan bari naje na kawota ,amma imam baka da hali ace wai har ƙafafunka su kasa ɗaukar ka amma ka gagara faɗa mun baka da lafia,."

"Tare suka dawo su uku,da ummu da KB da umaimah,"

Idan tace hankalinta bai tashi ba jin ummu tace wai kafafun sa sun kasa ɗaukar sa to ƙarya take.

"Zaune suka tarar dashi yana rirriƙe kai,da dan hanzarinta ta karasa tana Mai faɗin" Paki maine yake damun ka,and a matsayin ka na mai duba wasu Mai Ya saka Wasa da lafiyarka haka for God sake.

"Ki faɗa masa dai kila yaji naki Baiji nawa ba cos imam halin sa sai shi,

Kalan ummu yayi cikin shagwab'e murya wadda tasa umaimah mayar da hankalinta gareshi yace"ummu dan Allah zanci chips ban breakfast bafa."

Cikin kulawa tace bari naje nasa Emmanuel ya soya maka,

Cikin wata shagwab'ar yace "ummu please ni naki nake so bana cook ba,".

Murmushi tayi tace" naji ,bari naje nayi maka ,daɗina da ciwan ka dan banzan demanding,

Dr Umaimah ki duba munshi dan Allah ,kin gansa dai nan akwai raki da ragwanci.

Murmushi umaimah tayi cikin jin kunyar Ummu wanda ta rasa dalilin jinta .

Bayan fitar ummu Paki Ya kalli KB yayi masa alamu da ido akan Ya basu guri,

Babu musu KB Ya juya yana Mai smirking aransa yana faɗin"paki shegene".

Jawo stool umaimah tayi ta zauna tana Mai facing ɗinsa"tace mene yake damunka paki,?"

Kaifa ba yaro bane da zaka zauna a gida bayan kasan baka da lafiya and of course zaka iya bawa kanka kulawa why this.

Zuba mata ido yayi kafin yace"ke kike damuna,sannan ke ce kawai Mai bani maganin ciwo na sabida ciwan sanki ne Ya dameni Ya hanani fita ko ina,amma ganin ki ɗin nan da nayi Ya yaye mun duk abunda yake damuna ".

"I miss you ,ina san sakaki cikin idona ,ina san nuna miki kulawa ta da soyayya ta ,na gaji da punishing kaina da ƙin nuna miki soyayyata shi yasa nayi creating ciwo na,

Naga Kin damu dani kuma zaki zo ki bani magani?

Sai gashi kuwa kin zo,har gidan mu,har ɗakina ,Kin kawo mun maganin ciwona.

"Kallan sa tayi da mamaki tace "so dama lafiyarka ƙalau ka tadawa mutane hankali must especially ummu,"

This is childish Paki,and nazo nan as a doctor don't get it twisted .

"Dariya yasa yana Mai faɗin"Ai wata ƙaryar ba haramun bace tunda gashi Kin zo ganina ,wanda Ya tabbatar mun da Kin damu dani,shi kaɗai Ya isheni,bakiji yarda zuciyata tayi sanyi ba ""

"Addua kawai nake na mallakeki,kamar yarda kika shigo ɗakin nan as My doctor and lifesaver na shigo dake a matsayin matata .tunanin hakan kawai yana sani farin ciki".

Dan Allah umaimah,ki buɗe mun kofar zuciyarki na shiga na b'ata ki da soyayyata ,wallahi bazaki tab'a Allah wadai da hakan ba,

Zan baki dukkan soyayyar da kike mafarki a rayuwarki har da ƙari.

Ɗ'an Marairaice mata yayi da idanun sa kamar zaiyyi kuka yace "kinji umaimah na".

Saurin ɗauke idanun ta tayi jin yarda Abun Ya saka mata goosebump nan take,

Cikin rashin sanin abunda zata fada tace"na tabbata ba kaine na fari ba ko na karshe Stop acting like one".

Shafa gefen gyararren sajen sa yayi yace"im the 3rd born and kar kiyi using wannan topic ɗin as an excuse ki b'atar da maganan da nake".

"Ajiyar zuciya tayi tace"Paki zamu iya yin maganar nan a office ba sai kayi faking rashin lafiyarka ba kasa kowa a damuwa, kasa nazo gidan ku, wani idan ya shigo ya ganka haka ka sani gaba kuma yaji maganan da muke kasan we are in trouble ko?

"Za'a fara bawa clip din chan second thought,"

"Har a lokacin idanun sa akan nata Kafun yace"Umaimah,muna zaune ni dake a ɗaki ɗaya mu kaɗai trust me babu wani abu mara kyau a tattare dake a zuciyata,"Ina sanki ,ina girmmaki,ina ganin mutuncinki to the extent that bazan taba tunanin banza akan ki ba.

"Ya kamata kuma ace Kin sani,duk wani abu da wani zaice baya damuna ,sannan muddin kika ƙarbi tayi soyayyata bana tsoran kowa a duniya yasan ke tawace,"

Kin tuna ?

I even confessed to the board ,im not scared.

"Kamata yayi ace tayi mutuƙar jin haushin abunda yayi mata na sakata zuwa da ƙarayar ciwo,amma sai ta tsinci kanta da jin daɗin zuwan nata,

Lips Ɗinta na ƙasa ta mayar bakinta tace"im scared".

"So yaka Ya Kama hannun ta yayi assuring Ɗinta amma yana tsoran kar ta fara wani tunanin,"

Daga inda yake zaune yana facing Ɗinta yace"tsoran me?"

Tsoran kar na yaudareki?

Ko kuma tsoran abunda society zasu ce?

Ko kuma tsoran kar ayi ta maganarki ace kinyi Aure uku amma Kin wa saurayi wayau Kin Auresa?

Ɗaga girar sa guda ɗaya yayi cikin sigar tsokana lokacin da yayi maganar ƙarshen.

Murmushi tayi tana Mai saurin kai idanun ta ƙasa dan wata irin kunya Ya bata,Kafun tace "duka"

Ɗago idanunta tayi ta kalesa tace"look paki,im 29 kaima kuma you're  29 kamata yayi ace ka Auri macen da bata kaini a shekaru ba,

Paki kana ji da jini a jiki ,bai kamata ka ja rayuwarka baya ba ta hanyar shiga cikin tawa alaƙarba,

Kasan ni ne kawai as Dr Bulama amma Bakasan labari na ba,

Trust me ,im not the type da zakayi getting involved da,last mijina ɗan Blood money ne and har takaba nayi masa ,Family ɗin ka ma would never Approve of us. "

Saurin Mikewa tayi saboda zuciyarta ta fara melting wa Paki sannan cikin san kanta taji zuciyartata tana faɗa mata ta bashi dama ta jawosa rayuwarta amma baza tayi hakan ba .

"I think mu bar abun nan a nan ,yes na yarda im attracted to you ,i mean who wouldn't,amma im not that selfish ,so please paki mu yanke wannan alaƙar da baza ta haifar mana da ɗa Mai ido ba.

Hanyar fita ta nufa,da sauri yasha gaban ta yace "Im not perfect umaimah nasani i would never be perfect ,im not perfect amma na maki alƙwari zan baki dukkan soyayyar da nake da ita,

Nasan bazan taba impressing ɗinki da kuɗi ba amma i will spoil you with love,

Zan ɗauki su Nadiya kamar nawan Zan basu uba ,na miki wannan Alkawarin insha Allah."

Ban san labarin ki ba ke na sani sannan bazan takura akan dole sai Kin faɗa mun labarinki ba ,Zan jiraki duk ranar da kika shirya faɗan mun Zan saurareki sannan ki sani duk munin past ɗinki bazai dameni ba ,

"Society kuwa ,Forget about it ,ni Zan zauna dake basu ba,sannan maganar iyayena they are mine kuma nasan yarda zanbi dasu,"

Clip kuwa ,wanda Ya fasa bashi second thought, ni dake da ahalin mu Ai munsan dai dai.

.And yes Kafun na manta kar ki manta na baki wata ɗaya

Ki Amince dani dan Allah.

Yar ƙaramar dariya tayi tace "wata daya kamar shekara biyar yarda ka ke wani juyata,"

"Matsa na wuce and Zan kijiraka a asibiti da safe i will be expecting you.

Dan shiru yayi yana san gano abunda take nufi zai magana ya tsinkayi muryar Nana na faɗin Au har ƙurya suka shiga ?

Ke wacce irin uwace Habiba?

Zaki bar ɗanki da baligar mace.

Bari naje naci uban yar iskar yarinyar.

Da sauri Paki Ya matsa bakin kofar jin yarda Nana ke neman balle kasa kofa....

Chuchujay✍🏽

T

B

C.
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU

(a Hospital romance)

By

Chuchujay ✍🏽

Episode 1️⃣9️⃣➡️2️⃣0️⃣

Kamar guguwa haka Nana ta faɗo cikin ɗakin ,

Tsaye Paki yake gefen Umaimah dan tana turo kofar Ya matsa ,

Wani irin kallo yake bata ran sa a mutukar bace

Daga bayan ta ummu dake biye da ita tace "Nana yanzu Kin yarda imam baya da lafiya shine abunda Ya kawo umaimah nan ,amma ba abunda kike tunani ba".

Kallan ummu dake maganar Nana tayi kafun ta matsa gurin Umaimah wadda ta fara ja da baya dan bata manta cizan da Ummu tayi mata ba saboda yarda Ya bar mata tabo,

Shinshina ta Nana ta fara kamar wata kare Kafun tace "kwarankwatsa Habiba yarinyar nan kanshin turaren imamu take ,hakan kuma abu ɗaya yake nufi wanda Shine daga jikin sa take."

Cikin bacin rai imam yace "subhanallah ,Nana menene haka wai?"

Wacce irin magana ce daga jikina take?

Duka ta kai masa wanda yayi saurin kaucewa tace "dan ubanka babu abunda ban sani ba

musamman wanda Ya dan danganci mata irinta ,idan ba kinibibi ba uban menene Ya kawota duba imamu cikin gidan nan?

Ko ance mata bamu da likitan da yake zuwa duba mune ,

Wanda ma yasha gwagwarmaya a filin daga ,Ya samu horo na sojoji mazan fama masu jini a jika .

Kallan umaimah tayi wadda take ji a ranta da ace nana ba kakar paki bace ta daɗe da maganinta,

Cikin yin fiki fiki da ido tace sameera zo ki gane mun bakinta kamar sumba suka sha dan naga Ya kumbura ko ido nane?.

Da sauri sameera da ta biyo bayan su tace"zancen ki dutse Nana wallahi gashi nan da tazo bakin ta ba a haka yake ba ,ni dama tunda naga Ummu ta fito ,KB ma Ya fita nasan Akwai magana,amma nasan ummu bazata saurareni ba,ke kuma gashi baki gida,shi yasa kina shigowa naga Ya kamata na faɗa maki wannan zance kiyiwa tufkar hanci.

Wani irin kallo Ummu ta bawa sameera kafin tace"anya sameera za'a tafi haka kuwa ?,

Mene yake damunki,duka duka yaushe na bar su a dakin sannan menene laifi idan har likita da mara lafiya suka keb'e a ɗaki tare ?

Haba dan Allah muna yiwa mutane zato Mai kyau mana.

"Ba shakka habiba,ba shakka ƴar masu jan kunne har tasan wai ayiwa mutum zato Mai kyau,

Gaskiya Muntari nikam Ya cuce ni da Ya Auro ki,

Duk yan matan Fulani dake garin nan kyawawa Ya rasa wadda zai Aura sai wadda addinin ta ma yake da rauni,

Ke da baki da tarbiyya ina zaki samu damar bawa wani,?

Kan umaimah ta kuma yi wadda ta kai maƙura ,ta ɗaga hannu zata mareta tayi saurin rikewa.

Wani karamin murmushi tayi a yayin da Nana ta saki baki tana Mai rafka salati,

Sauke hannun nata Umaimah tayi da nutsuwa tace"Nana ke babba ce ,sannan ke kaka ce,kuma a matsayin ki na Nana'n imam na ɗauke ki kamar tawa,dan Allah ki bari sannan duk abunda kike tunani bashi ne Ya shiga tsakanina da Imam ba,ni ina da abunyi a asibiti ,

Kallanta ta mayar kan ummu tace "ummu imam is okay yanzu sannan Zan bawa KB magunguna Ya kawo masa ,stress ne kawai yake damun sa."

Murmushi ummu tayi tana Mai jin umaimah a ranta kafin tace"na gode My daughter,Allah yayi miki albarka.

Wani irin daɗi umaimah taji a lokacin da ta saka mata Albarkar dan rabonta da jin Kalmar nan gurin uwa har ta manta,

Jakarta ta ɗauka tana mai mayar da kallanta kan imam Kafun tace Allah Ya ƙara sauki ,sai na ganka a asibiti, "

Cikin zaƙuwa yace "insha Allahu gobe zaki ganni,ai tunda kika zo na warke ."

Murmushi tayi masa ta ɗauki hanyar fita a ɗakin ,

Tana isa falon da suka zauna da ummu taji muryar Nana na faɗin"hylloooooo,ɗiyar Yan marasa kunya ni zakiyiwa fitsara cikin gidan ɗana ki fita Hankalinki a kwance bansa an karya mun ke ba."

Appan ,Appan maza zo nan ,zo zo yau akwai bala'i an zagi uwar ubanka,

Affan da suka dawo daga unguwa da Nana wanda baisan wainar da ake Toyawa bane Ya fito da saurinsa jin tana kwala kiran Appan kuma tana faɗin ana zagin ta Ya fito da saurinsa yana faɗin"Nana wanene wannan yake zaginki na miki maganinsa?"

Turus Yayi ganin umaimah ,kallo ɗaya Ya gane fuskarta dan shi ba ma a case ɗinsu Ya santa ba dama tun tuni shi A wani hira da ka tab'a yi da Alhaji Bulama Along side da ita take burgesa musamman da ake faɗan nasarorinta As a young female surgeon Mai ƙarancin shekaru.

Dr Umaimah Bulama a gidan mu?

Wow wow,dafa Paki da Ya biyo Nana tare da kowa yayi yace "hamma ita ce dama Dr Bulaman, da kuke aiki tare,God wallahi kina burgeni,

Takawa yayi zaije gurin ta Nana tasa hannu ta kamo masa hular sweater ɗin dake jikin sa tayo baya dashi kiiiiii tace"Ubanka muntari,

Ni zakayiwa ɗiban albarka da rana tsaka,to sai in gani idan ni ko ita,nan a ɗakin imam Babu irin wankin babban bargon da batayi mun ba,sannan har gida ta biyo Yayan ka ta lalatashi.

Saƙalo dukkan su sukayi suna mamakin yarda Nana bata kunyar gandara ƙarya.

Har Umaimah ta juya zata tafi dan bata iyawa Nana da harigidonta taji an sake fincikota,

Imam ne yayi yunƙuri yana Mai faɗin "wai Nana menene hakan?

Nuna sa tayi da yatsa tace "kul ka kiyayeni,wallahi naci maka mutunci yanzu ,tunda dukkan ku kuna ganin kun kai akan karuwa zaku juyawa uwar uban ku baya,To wallahi ni nasan maganin ta ,sai taji dama bata kawo kanta iskanci gidan nan ba ,dan sai nasaka TEGA Ya cizar mata ƙaffafun 'da suka kawota.

Fincikar Umaimah ta farayi har sai da ta kaita Harabar gidan,a karo na farko umaimah tasa hannu ta bige na Nana wadda reaction ɗin Ya kuma zaubarata,

Cikin jin zafin kiranta karuwa da tayi tace"Nana ni ba karuwa bace ,ki tambayi jikanki,

Murmushi tayi da wani abu Ya ɗarsu a zuciyarta ,Ya kamata ta bawa tsohuwar nan maganin larurarta,

Kamo hannun Nana tayi guda biyu tace "ina ta gujewa amma Nana kinƙi bari kinsa dole sai na faɗa miki gaskiyar abinda yake faruwa tsakani na da Imamun ki ,"

Petting hannun Nana tayi tace "nasan rashin sani yake saki yi mun komai,bari na sake gabatar miki da kaina,".

Sunana Dr Umaimah Bulama ,ina harka ne ta farka mutane da ɗinke su a babban asibiti dake cikin garin nan na Adamawa,

Ni bazawarace ,sannan nayi Aure ɗaya ɗaya har uku,

Ɗan karamin murmushi tayi ganin yarda Nana ke mata wani irin kallo tana mai san kwace hannunta a nata ta kasa duba da yarda ta damke hannun sosai tace "A'h bari kiji Nanan mu,a kowanne Aure da nayi sai da na haihu,

Na samu Nameer ,Nadiya da Abdallah,sannan a duk mazan da na Aura akwai tarihinsu ɗan daya ma yana cikin kungiyar tsafi,

Kwalalo ido Nana tayi jin maganar tsafi ga kuma yarda Umaimah ta damƙe mata hannu inda ummu da Paki da Affan suke gefe suna kunshe dariyar su,

Sameera kuma na kusa da Nana tana zazzaro ido kamar an kaɗa jab'a buta.

Wani murmushin gefen Baki umaimah tayi ta ƙara matsowa kusa da Nana tace "wani abu da zai miki daɗi Nana Shine ni da Paki muna soyayyane sannan ina san na Aure miki shi na mayar dashi mijina na sunna kinga da haka zaki yarda ni ba karuwa bace tunda komai zai faru tsakanin mu sunnah ne,"

Ki yarda Nana'mu Ina san jikan nan naki sosai ,sakar hannun Nana tayi guda tace "zan mutu idan ban zama matar shi ba,"

Nasan da kikaji daga baki na zaki amince da Auran Imam da Umaimah dan na ƙosa nayi maki tausa.

Sake matsa hannun Nana tayi kafin ta jawoshi saitin bakin ta ta sumbata,

Fincike hannun Nana tayi tace "uban ubaki dan kan uwaki,kina kallo ko habiba,ba nace miki yarinyar nan yar iska bace ,kuna kallo kuna kuma jin abunda ta mun sannan ta faɗa ko,

To wallahi sai dai kiyi bunga ,kiyi funfuna ki rub'e babu Aure akan mu baki ɗan mu,wanene Ya faɗa maki mu shashashune da basu da tunani,

Dan ubanki ina kika taba jin wannan gambizar,duk kinyi kwararo a hakan kike so ki Auri yaran da yake sabo fes a leda,wanda nayi imani da Allah yana kaffa kaffa da kansa baya iskanci.

Wallahi sai dai ki mutu sau ɗari 'dan muddin in ni nayi cikin muntari kuma na haifesa a cikina nayi rainan sa wallahi bazaki Auri imamu ba. "

Wani murmushi umaimah tayi tace "yanzu da kanki Nana kinga kin gyara maganar da kikayi na muna iskanci nida Imam a ɗaki ,tunda Kin yarda shi sabo fes ne a leda kuma yana kaffa kaffa da mata ,kinga kuwa lafiyar sa kawai na duba a ɗakin chan sai kalaman soyayya da muka faɗawa juna,

Ba komai Nana,ni na yafe miki tunda dai kinga inda daf da shigowa zuri'ar ki dole na maki ladabi na soki na kyaunace ki,

Ni umaimah ina sanki har raina Kaka ta gari".

Ai kamar ta kuma chinno Nana cikin Balai tace "wallahi karyarki yarinya ,imamu da kike gani jelar raƙumi tayi nesa da ƙasa sai yarinya irin sa,"Jawo sameera tayi gabanta tace"kinga wannan to irinsu ne ake faɗawa tubus tubus ba irinki marau marau ba,iyhe,"Kuma ki gaggauta barin gidan nan Kafun wallahi na sa a sako mun karen Chan TEGA Ya ciccinye mun yar banza.

Juyawa umaimah tayi ga ummu wadda ke ta faman guntse dariyar ta ganin Yarda Nana ke hakikancewa tana maidawa umaimah magana,

Zata so ace maganar da Umaimah ke faɗa gaske ne ,ita kanta ta gaji da Nana da halinta,tasan Umaimah ne zasu gwara tare amma ita kam Nana tafi karfin ta.

Murmushi umaimah tayi tace "ummu ni Zan wuce".

Murmushin ummu ta mayar mata tace "Allah yayi maki Albarka."

"Ai kamar Ta sake hasala Nana ta Kalle ta tace "idan ke zaki sashi yayi mata Albarkar habiba 'dan Allah saka shi,Ai Albarka tayi gabas wannan fitsarariyar yarinyar tayi yamma ,"

Murmushi umaimah ta kumayi tana jin daɗin shaƙar da Nana wadda takai maƙurar shaƙuwa,

"Ina sanki Nana,Sosai ,Kema ki samun Albarka na bar gidan nan da soyayyar mutane da dama,nasan kaima Affan ka karb'e ni ko?"

Tamayar da tambayar ta ga Affan.

Dafe saitin zuciyar sa Yayi yace "In a heart beat,Adda Umaimah".

Kamar Nana zata haukace haka ta juya tana Mai zagin Affan Kafun ta jawo hannun Paki Ya dawo yana Mai facing Ɗin umaimah tace "maza faɗawa wannan fitsarariyar guzumar baka santa sannan kajata kamar shara ka fitar mun a gidan nan".

Kallan Umaimah yayi cikin ido yace"Ina Sanki sosai Umaimah na ,idan na rasaki na tabbata Nana zata rasa ni 'dan mutuwa zanyi,gobe da safe insha Allahu da fuskata zaki fara karin kumallo cos nasan halin ki baki san cin abinci ,amma idan nazo da kaina Zan baki a baki.

Wani irin sautin Awwnnnnnnn da aka saki daga baya ne yasa Umaimah juyawa,

Afnan ce Tare da KB suna masu shigowa daga waje,

Da gudu Afnan ta ƙaraso ra rungume Umaimah tace "get married to My brother already please ,murmushi Umaimah tayi tana Mai kalla Nana wadda ke tafarfasa kamar zata fashe,

Raba jikin ta tayi da na Afnan tace "sweety you're so cute and kar ki damu nan da sabuwar shekara ni da Hamman ki zamuyi Aure kinga lokacin mun cika 30 years tare ,wata guda kawai ya bani,"

Cike da adoration Afnan tace"mafarkina hamma Ya samu,ina san na Auri age mate ɗina".

Cikin jaraba Nana tace"kan ubanchan,Shekararki Ishirin da tara ma,kike tsaye nan cikin rashin jin kunya kike maganar Auren Imamu,"

Ke ki fita a idona na rufe 'fa,

Kai kuma Imamu wallahi sai anyi saban lale 'dan wallahi ko ni ko ku,

Ke kuma Afnan zanji dake ne ,

Juyawa tayi tana Mai cewa sameera "ke wuce muje ,bari na kira muntari duk abunda yake yazo gida yaji abunda iyalinsa suke mun da wata karuwa a Chan waje,Zan nuna musu na haifi ɗa sannan Ya haifu."

Kallan ummu umaimah tayi tace "im sorry ummu ba niyata nayi disrespecting Nana ba,i just couldn't stand it,amma kamar na wuce limit ɗina".

Murmushi ummu tayi tace"ki kwantar da Hankalinki kar ki damu ,'in dai Nana ce haka take a kullum .

Sallama ta musu tana Mai tsintar kanta da cewa imam"ina jiran zuwanka gobe."

Chuchujay✍🏾

T

B

C.

Join my whatsapp Channel inda zaku samu tukuicin littafina na noorurrahman wanda yake paid ne,amma zan sadaukar maku dashi kyauta,

Ina masu cewa suna san karantashi amma sabida na kuɗine basu samu ba.

Ina masu neman discount ,
Yanzu ba babu buƙatar wannan duka Just Join my whatsapp Channel domin samun sa kyauta.

https://whatsapp.com/channel/0029Va9RLKT2P59fHSa7Ia1j
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍: AURE UKU

(a hospital romance)

By

Chuchujay ✍🏾

Episode 2️⃣1️⃣➡2️⃣2️⃣

Gaskiya Dr Bulama bazan iya Wanchan Aikin na cyst ɗin chan ba ,patient Ɗin 'fa Hiv positive ce Fa,

Gaskiya i cant risk it kawai idan zakiji shawarata muyi mata transfer ko kuma mu ɗorata akan magani,

Gaskiya bazan iyawa Mai HiV operation ba ,

Sauke glasses ɗin dake idanun ta umaimah tayi ta kalli Dr maryam dake ta faman mitar abun,

System ɗinta ta juyo tana mai Kallan Dr maryam kafin tace "Dr maryam ki kalla da kyau,cyst ɗin matar nan yayi girman da idan ba'a cire ba zai zama cancerous,

And 'dan kawai tana da Hiv shine baza'ayi mata aiki ba?

Wanne policy ne Ya hana ,?

Shikenan shi kuma Mai HIv ba mutum bane baza ayi masa aiki ba idan yana neman a cecesa?
"

We have precautions to follow kema kin sani,to menene zai sameki dan kin mata Aiki,bana tunanin zaki mutu.

Okay naji its okay,kar kiyi i will take the lead,you can leave My cabin.

Tashi umaimah tayi 'dan zuwa nurses station ,alamu tayiwa farouk Da yazo,

Babu musu Ya taso yazo,cikin serious tone tace "zamuyi wa matanan aiki ,nasan baka da komai in schedules naka ,Dr maryam baza tayi ba so we are taking over ASAP arrange my team and prepare the operation theater,na tura maka details ɗin patient ɗin ,"

SOME HOURS LATER.

Ko wannen su dake cikin OR ɗin sanye yake cikin gowns da aprons ,eyes wear,da face shield saboda gudun splash na jini,ko wani fluid na jikin mara lafiyan,sanann kowannen su hannunshi sanye da glove,

Tsaye umaimah tayi akan Patient ɗin Kafun tace "Intern students This Patient is HIV positive, and zamuyi mata Aiki mu cire ovaries cysts ɗin da take dashi,so beware of needles injury, scalpels ko wani sharp object ɗin ,so Aikin nan tare zamuyi its high time ,ku kula needles Are not allowed to be bend da hannu,ko cirewa jikin syringe,

Puncture resistant container ta nuna tace duk used abu na disposing Ya kasance anan. "

Nurse farouk dake gefanta ta kalla wanda tasan He's Good at his work and komin menene tsananin risk na Aiki zaiyyi indai tana gefen sa ,itace tsananin yardar da sukayi da juna,

Kaɗa mata kai yayi Kafun tayi murmushi,

Paki  wanda tunda ya shigo asibitin bai sata a idanun,sa ba sai da aka kirasu ,har cabin ɗinta Ya gama zagayen duniya bai ganta ba,

Matsawa gefenta yayi cos shima Ya yarda indai da risk to Ya same su a tare.

Murmushi tayi ganin abunda yayi,

We are performing laparotomy instead of using laparoscopy since the cyst is large,

Alamu tayiwa Nurse farouk wanda Ya fara bata kayan aiki tayi makin large cut a tummy ɗin patient ɗin wanda take jini Ya fara fita,

Komai Ya dawo visible gareta tana gani a haka ta ciro Cyst ɗin,tasa a container ,miko hannu da tayi yasa paki dake adoring ɗinta mika mata abunda Zatayi staples ,

Kallan Dr Munnir tayi wanda yayi saurin ɗauke ido dan kar tace yazo yayi dan haka kawai ta maida hankalinta wajen staples ɗin.

Bayan ta gama tace"our surgery is done,"

Nurse Fatima take this Cyst and ovary  to the lab a duba ko cancerous ne,amma im positive its not ,cos idan Ya zama cancerous ne we will have to remove her womb,.

Fita tayi ta barsu su karasa inda tana sa kafa paki Ya saka,

Apron da Face wear ɗinta tayi disposing ,wash room ta shiga bayan ta cire gloves tana Mai saurin wanke hannunta throughout,

Bayan ta gama ta fito,

Gabanta Ya bayyana yana Mai faɗaɗa mata murmushin sa yace"i Love everything' about you Dr Bulama,"

Juyawa tayi ganin mutane na wucewa tace"Paki mutane zasu jika 'fa,"

Karamar dariya yayi yace"I dont Care ,su jini,ko Kin manta abunda na faɗa a gaban management,ina sanki,and bazan daina ba ,sannan a da ni kaɗai nake yi amma yanzu mun zama mu biyu,"

Kaɗa kai tayi ta fara takawa zuwa cabin ɗinta inda shikuma yake binta a baya,

Kowa kus kus ɗin yake saboda maganar da yafaɗa na yana santa Ya fito waje ,wasu su zageta wasu kuma suji haushin ta saboda samun Paki dan akwai masu crushing akan sa da yawa.

Zama tayi kan kujerarta yayin da Ya zauna a wadda take facing Ɗin ta yana Mai ƙin ɗauke idanun sa akan ta,

"Akwai wani abu a fuskana?"ta tambaye sa tana mai ɗaga masa gira,

Dan rufe idanun sa yayi kana Ya buɗe yace"kyanki da yake ɗaukar hankalina a kullum ,Shine a fuskarki,."

A kalla yasata murmusawa na babu adadi,dan Cije lebenta na ƙasa tayi tace "baku da wani abu da zakuyi ne yau".?

Shafa kwantaccen sajensa yayi yace "Well duk Abunda zanyi yana tare dake Kin manta kece ogata,sai yarda kikayi dani,komai nawa na ɗamƙa miki ,sannan duk inda kika saka ƙafarki nan Zan saka tawa,"

And yauwa inasan san na tambayeki,

Ina fatan kina nufin duk wani abu da kika faɗa jiya gaban su Ummu,cos ummu ta gama saka rai dake ,haka zalika siblings ɗina,

Kowa yana sanki amma babu wanda ya kaini sanki,so please kar ki janye maganar ki na jiya duk da ina da yaƙinin dan Nana kikayi amma na tabbata Wani bangaren gaskiya ne,

Kallan sa tayi cikin ido tace"yanzu idan nace kazo ka Aure ni zaka iya?

Dafe zuciyar sa yayi yace"cikin bugun zuciya,i want to wife you sannan inasan muyi 30 years a ɗakin mu Im not joking cos duk Abunda Ya shafe ki ni bana ɗaukar sa abun Wasa,ko gobe kikace na Aure ki Zan yi ,trust me im loaded,

Ƙaramun murmushi tayi tace "Im not After your money kaima ka sani ba,and i Just dont want to rush things' dan haka you will have to court me,Ya kamata kasanni sosai nima nasan ka ,like da dislikes ɗin ka da nawa,and a side ɗina bani da matsala ,side ɗinka ne " .

Karshen maganan ta kai tana san ganin reaction ɗin sa Kafun tace "Im Sorry idan jiya na wuce iyaka".

Yar Dariya yayi yana Mai tuna abinda Ya faru jiya Kafun yace "Well indai kin yarda dani,kin kaini gida a matsayin wanda kika zab'a zakiyi rayuwa da then nana baza ta zama matsala ba."

Ɗan kasa tayi da murya kafun tace "beb ɗin ka fa".

Fahimtar da sameera take yasa shi darawa yace"na jiyo kamshin kishi,Well sameera bazata taba zama threat tsakanina dake ba cos ke nake so ,sannan ni tsakanina da ita babu wata alaƙa ta soyayya,kawai alaƙace ta zumunci bayanta ba wata ,sanann tana internship ɗinta ne a sydney private hospital wanda na Uncle ɗinta ne and saboda tace a gida nan ɗin zata shi yasa suka barta,

Sannan gidan mu sun bata masauki ne saboda sun ɗauketa an zama ɗaya duka daga Family ɗinta,

Dan shiru tayi tana nazari ,ba wai tana tsoran Sameera bane,amma tabbas tasan akwai sauran rina a kaba,

Fitar da tunanin sameera tayi a kanta kafun tace"you have to try hard to impress me 'fa paki cos na wuce stage ɗin da puppy love zai burgeni, "Can you handle me.

Haɗe hannayen sa biyu yayi yace "ban fito ba sai da na shirya sannan ki yarda dani idan nace maki,bazaki tab'a tsallake soyayyar Paki ba."Kashe mata ido ɗaya yayi a ƙarshen maganar sa wanda Ya sakata giggling kamar wata high schooler,

Buɗe kofar da akayi ne yasata saurin juyawa akan kujerarta tana Mai Kallan desktop ɗin dake gefen ta cikin Mazewa,

Nurse farouk ne,haɗe rai tayi tace "yaushe kafara shigo mun babu Knocking ,"Karamun murmushi yayi dan Ya fahimci abinda yake faruwa,

Aje file ɗin dake hannun sa yayi yace "ayi mun afuwa to,file ɗin patient ɗin chan ne hardcopy na kawo miki kamar yarda kika buƙata,".

Na barku lafiya ,da murmushi a fuskarsa Ya fita.

Bayan fitar sa Paki Ya Kalleta yace"masoyiyata ki daina ƙokarin boye soyayyarmu dan yanzu abunda nake faɗa miki,kowa a asibitin nan yasan ina sanki,sannan a yanzu ma na sake ɗaura ɗamarar sanar da kowa soyayata gareki,

Tashi yayi yana Mai blowing mata kisses da hannu ,Kafun Ya kama hanyar fita yana Mai faɗin we are going out for dinner yau  since yau kina night ne".

Kaɗa kanta tayi bayan fitar sa dan rabonta da jin yanayin da take ji game da paki tun kan Hafiz.

A hall ɗin da suke zama Ya tarar da KB tare da Aisha shareef suna hira ,tana ganinsa ta washe masa haƙora tace "paKi ina kaje ne tun ɗazu ina nemanka since operation ɗin chan bangan ka ba,"

Zama yayi kusa da Kb yace "nace zance ne."

Cikin rashin jin daɗin furucin nasa tace ,zance mana,naje zance gurin macen dake haukata mun lissafina a kullum idan na saka ta cikin idanuna,

Ina tare da Dr Bulama tun ɗazun ,da kyar na iya yakicewa na taho saboda nasan yanzu Zatayi abu Mai muhimmanci ne.

Da mamaki ta kalle sa tace"dama wai paki jita jitan nan ba karya bane,kai yanzu baka jin kunya ma?tayaya zakayi soyayya da bazawara wadda tayi Aure daya daya har uku ,har da ƴaƴanta fa,

Amma kai ka kalle ka young,handsome and rich,Mai zai hana ka kalli matan dake gabanka.

Shima da mamakin furucin nata yace "kina nufin yan mata irinki Zan kalla?kalli nan Aisha,I hope ban baki wrong signal ba,sannan with All due respect bana san kina faɗan abun banza akan Umaimah raina zai na baci naji bana san magana dake ,and yes ke ba irin matan da nake so bace ,irinta nake so dan haka respect it please."

Dauke kai yayi da Ya gama maganan sa dan ta ɗan Sosa masa rai,

Tashi tayi tace "kayi hakuri ban faɗa bane da wani abu,"

Bayan barinta gurin KB ya kallesa yace "mutumina why mana,Mai yasa zakayiwa Aisha magana a haka ne saboda Allah."

Haɗe rai yayi yace"gwara nayi rejecting ɗinta tun kafun ta ɗauki hope ɗinta da nisa,ni one woman man ne,one army"

Dariya KB yayi yace "zaka sani ne duk ranar da Nana ta mayar da kai sameerah and umaimah man".

Ƙaramun tsaki yayi yace"bismillah ɗin ta tasan halina ai".

Dariya sukayi a tare kowa da abun yake tunawa na Nana.

***

Kamar yarda Ya faɗa da dare Ya fita da ita romantic dinner,

Duk yarda take tunanin Paki Ya wuce nan gurin saboda yarda yake narkar da ita a soyayyarsa

ba a magana,har asibiti ya maida ta cikin kulawa yana mai nuna mata matuƙar soyayyar ta da yake yi.

Sai wurin 9 Ya shiga gida,

Yana ƙokarin shiga sashensu yaji An ambaci sunansa da muryar da ya Jima bai ji a zahiri ba illa a waya.

A/N

Mundai kusa Aurawa paki umaimah and nan zamu tsunduma tafiyar Aurenta da paki,daɗi ne ko akasin haka?.Nidai nace daɗi ne kufa?

Ku cigaba da bina kun sharhi dan ina mutuƙar kaunarku da sharhinku❤

Chuchujay ✍🏽

T

B

C.
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍: AURE UKU

(a hospital romance)

By chuchujay ✍🏽

Episode 2️⃣3️⃣➡2️⃣4️⃣

Hamma ?

Da gudu Ya nufe sa Ya rungume yana Mai faɗin"Im not dreaming hamma ne a gidan nan,oh My God,"

Tapping kafaɗar sa usama yayi yace "come on wani ya jika sai yace bana zuwa gida kwata kwata,

Naji dai it been a long time amma not long ɗin da kake exaggerating,

Cike da farin ciki imam yace"koma dai yayane hamma i really really miss you and kazo a dai dai lokacin da nake bukatar ka,"

" I hope dai nima ina Cikin waɗan da kake buƙatar gani,

Juyawa yayi da sauri yace intiiii?

Murmushi tayi tace uhum Hamma Imam Ai ni na kusa fushi da kai tunda baki ɗaya Kama dai na nemana ko zuwa kawo mun ziyara,

Kallan cikin ta da yayi nauyi yayi yace "amma dai sai Kin haihu zawan nan da kikayi cos nasan halin ku mata da san zuwa gida yayi cikin farko,"

Shafa cikin tayi tana Mai murnar ganinsa Kafun tace"well kusan haka ,dama ina san zuwa gidan sai na haihu na koma amma this is not a coincident ka ganni tare da Hamma rana ɗaya munzo gida ,Nana ta kira mu amma Ba musan menene musababbin kiran ba,so dama ina san zuwa nayi amfani da damar If not karamun kiran nana da nasan rigima ce bazai ɗauko ni daga Kenya ba Ya kawo ni Nigeria,"

Dariya suka saka a tare dan kowa yasan halin rigimar nana,

Ɗaki intessar ta wuce dan wani irin bacci take ji,

Kallan usama paki yayi yace"hamma spend the night 'in my room nayi missing ɗinka and we have alot to talk about,"

Kaɗa kai Usama yayi ya mara masa baya,

Hamma mutanen Lagos,amma dai kai ɗaya kazo?

Kaɗa masa Mai yayi yana Mai ɗanewa gadan Paki yace "yea madam aiki sannan yara makaranta ,nima dole na yakice nawa aikin dan yanayin da NANA ta kirani nasan ba lafiya ba cos kuka take Sosai wai an shiga tashin Hankali mara iyaka a gidan nan nazo 'in ba haka ba Zan ga gawawwaki,i thought tun a gate zanga gidan nan na ci da wuta."

Dariya Sosai paki yasa yace"ku cigaba da biyewa waccan rikitacciyar tsohuwar, halin Nana

kuma wannene baku sani ba,ni na tabbata akaina ta kira ku saboda ina san wadda bata so na so kamar ita zata mun zaman Auren,Nan babu irin mitar da batayi akan naki Aure ba ,gaka da yara ga intee da ciki ni ina zaune,

Nan har cewa tayi mata nake bi,to tunda na kawo matar Aure Ko wacece abarni na Aura mana indai ba rigima ba.

Yar dariya Usama yayi kana Ya juyo yana Mai facing ɗinsa yace"who's the lucky girl wadda ta sace mun zuciyar dan kanina" .

Murmushi yayi yace "hamma lucky guy dai ,cos nine nayi babbar sa'a muddin akace na Aureta,Bro nasha Wahala Kafun na samu ta fara sakar mun duk da har yau bata fito fili ta kalleni tace tana sona ba,amma ni nasani na ƙarbu."

" Uhum yarda ƙanina ke bani labarin nan na tabbatar Ta haɗu,zan so na ganta,

Ƙara gyara zama paki yayi dan an Sosa masa inda yake masa kaikayi Kafun yace"Hamma case ɗin chan da Abbu ya kira ka akai wanchan karan na clip ɗina da itane ,and damuwar Nana ɗayace wai ta yi Aure har sau uku sannan tana da yara guda uku,and Im just a month older,amma hamma abun da za'a duba anan Shine wallahi idan na rasa ta Bansan Ya zanyi ba,trust me wani ciwan zai iya kamani na mutu."

Dan shiru usama yayi na wani lokaci kafin Ya faɗaɗa murmushin sa Ya dafa kafaɗar paki yace "brother as far as you love her just go for her,live your life ,babu fa wanda zai maka rayuwa,kai zakayiwa kanka,so chase it and have it and na baka dukkan wani suport ɗina,ina Tare da kai a duk wani step da zaka ɗauka a rayuwar ka,kawai ka tabbatar you're sure about it. "

Nima ina Tare da kai Hamma imam ,i will support you and we will beat Nana to it,

Muryan Afnan yayi echoing cikin ɗakin a yayin da yake shigowa ciki,

Kallansa imam yayi yace "lab'e ka koma kai kuma?"

Takowa ciki yayi yace"Ba lab'e ba nake bafa ,i Just got to overheard something and yau Brother's night ne shiyasa nima nazo a yi dani,

Sai a lokacin suka kula da pillow ɗin dake hannun sa,dariya suka sa a yayin da Ya shigo cikin yana Mai darawar shima,a haka sukayi ta hirar yaushe gamo har bacci Ya daukesu ".

******

Washe gari kamar yarda Iyalan Paki suke karin kumallo a yau ɗin ma haka ne,sai dai a wannan

karan baki ɗayan su ne suka hallarta ciki kuwa har da sameera yar karo wadda ke ta faman shishigin ganin yan uwan Imam sun karb'eta dan yarda Nana ta saka mata Auran imam gani take kamar ta Aure sa an gama,

Hatta Abbu da bai gari sai da Ya amsa shamacin Nana,

Bayan addua babu abunda kakeji na surutu face karar cin abinci,bayan sun gama  Nana ta miƙe tana Mai faɗin"kowa Ya sameni a babban falo ".

Babu musu kowa Ya hallarta duk da kuwa sun san sarai rigimace,

Zama tayi ta ɗora kafa ɗaya kan ɗaya Kafun ta kalli Afnan tace "ke tashi kije ki kira sameera Ya Ana zama na ahali zata ware kanta?.

Wani irin kallo Afnan ta mata kafun tace "bana tuna lokacin da kika haifi Daddynta ko mummynta,"

Tsawar da Abbu ya daka mata ne yasata tashi zuwa kiran Sameera tana Mai jin haushi,

Gyara zama usama yayi yace "Amma Abbu banga inda maganar Afnan tayi rashin dai dai ba,Nana fa taso mu tayi ta katse mana dukkan wani aikin da muke Mai amfani ta kawo mu nan dan yin magana mai muhimmanci,mene na sako wata sameerah?

Wacece wata sameerah ma?"

Cikin fushi Nana tace"uwarka Habiba mara ɗa'a ɗinchan ce Sameera usama,"Nace maka uwarka habiba.

Duk yaran gidan babu Mai fushin usama dan muddin Nana ta zagi Ummu gabansa baya b'ata lokaci wajen nuna fushinsa,cikin fushi Ya tashi yana Mai faɗin"Nana nazata komai Ya chanza shekara talatin da shida kenan fa!

Yakamata ki gane a yanzu da baya ba ɗaya Bane ,a da muna yara bamu fahimta,yanzu kuwa Ummu na da yaro Mai shekara talatin da shida idan baki ɗaga mata ƙafa dan komai ba kya ɗaga mata dan yaranta,babu yarda za'ayi muji daɗi muna zaune kina aibata mana uwa.

Baki tab'a kaunar ummu ba kamar ta kashe miki wani,Mai tayi miki?

Babu 'fa abinda ta tab'a miki illa zuri'a da ta bawa yaran ki,menene laifinta?

Gaskiya bana jin daɗin irin abunda kike yiwa Ummu Nana .

Kallan Abbu wanda yayi shiru yayi yace "kayi mun afuwa Abbu akan abunda na faɗa sannan ni Zan wuce dan na bar aiki sosai a company na dan Kafun nazo nan ma meeting biyu na ɗaga."

Ya juya zai bar falon Ya jiyo muryar Nana tana Mai faɗin"ɗan kundun uba Mai shegiyar baƙar zuciya Ya ta kakan sa,Ai sai kayi hakuri ka dawo muyi abinda ya kawo mu sannan indai Habiba ce Zan yi ƙokari naga ban faɗi abu mara daɗi ba akan ta har ka juya kuntacce."

Usama ka dawo ba!.

Muryar Ummu wadda taji daɗin tsaya matan da yayi ta Katsesa,

Dawowa yayi Ya zauna yana Mai faɗin "Allah yasa shima zaman ba wani rigimarki bace".

Yana ƙare maganar Sameera ta biyo Afnan,gefe Nana ta nunawa Sameera tace"zo zauna yarinyar Arziƙi,"

Babu musu kuwa ta dawo ta zauna.

Gyaran murya Nana tayi tace"Muntari maganar nan ce dole na yita, Maganace kuma da ta danganci imamu,matsar kwalla ta fara tace "muntari Nidai nasan ni na haifeka sannan kai yaro ne Mai biyayya,"Bawai ina san haɗa ka da iyalin ka bane amma da kaga abunda Ya faru dani jiya sai kayi kuka,

Wannan karuwar yarinya diyar Bulama jiya Bakaga rashin mutunci da tayi mun ba,kuma habiba na gurun haka zalika imamu, apan wa Apnan ,wallahi baka ji ɗiban Albarka ba har da cewa babu wanda Ya isa Ya hanata Auran imam ta maidashi waina sai yarda ta juyasa,

Shi yasa nikuma tunda na san wadda imam yake so tun jimawa wato Sameera shi yasa na kiraku gaku ga ita nan ayi magana a saka iyayenta a ciki ayi Auren su nan da ƙarshen wata guje ma shaiɗancin ɗiyar bulama .

Cikin bacin rai Abbu yace"habiba maine ke faruwa."

Affan ne dake gefe yace"haba Abbu kai kasan babu wanda zai zo har gidan,nan Ya zagi Nana bamu ci,masa ba,and Wallahi Abbu ba wai ina karyata Nana bane amma wallahi Adda umaimah bata zagi Nana ba ".

Cikin harzuƙa Nana tace"uwar Adda ba dai Adda ba,kaga muntari ni ba wannan ba ,muddin imamu yana san nayi shiru da maganar nan sai Ya Auri Sameera dan ba zamu saka ido ba Ya Auri zawarar da tayi Aure uku har da ƴaƴa uku,

Wallahi bazai sab'u ba,idan Ya sab'u kuma mutuwa nayi.

Allah Ya kiyaye,yarinya ƙwara yar shekara talatin bazawara?

Badai a zuri'a paki ba.

A Karo na farko ummu tace"idan yana santa kuma 'fa Nana?"Mene aibun dan Ya Auri Mai yara uku,bafa zunibi bane,abu ɗaya zamu duba shine suna san juna to mene Ya rage kuma?

Cikin fitina Nana tace "ke dallah rabu dani da tunanin ku na yahudanci,imamu bazai taba Auren ɗiyar Bulama ba,sameerah zai Aura".

A karo na farko intisar dake fama da kanta tace "amma Nana babu Ya hudanci 'dan hamma imam Ya Auri bazawara indai har yana santa sannan indai har ta ɗebo raban sa sai fa ta saukeshi,idan kika matsawa yin Allah sai kiga kamar yarda kika faɗa sai ki mutu ayi , Haba Nana kefa musulmace ,ko Kin fi san su samu rabansu ta hanyar banza?

To su samu Mana inti,ke nifa da Ya Auri yarinyar nan gwara Ya je Chan su watse su da Allahn su sannan babu mai kawo mana ɗan zina mu ƙarba,kilan ma sauran ƴaƴan duk a haka aka same su,sannan kiji da kyau Intii tunda na kai yanzu mutuwata ba yanzu ba nayi imani da Allah ,'dan jikina na bani habiba ma sai ta rigani tafiya!

Nana ta Faɗa tana Mai faman hura hanci kafin tace"muntari ,usama ku nake jira kuyi magana 'fa."

Ƙaramin dariya usama yayi yace"Nana wannan yasa kika kiramu dama"?

Ni dai babu abunda zance illa Abar imam Ya Auri wadda yake so,After all imam ne zai zauna da matar sa ba kowa ba Ko me kace Abbu?

Ni ganina abun nan Ai ba Mai wahala bane.

Idanun Abbu akan paki yake wanda ke goge kwallarsa gudun kar a gani amma hakan bai hanasa gani ba.

Gyaran murya yayi yace "yanzu Nana Ya kike so ayi,"?

Kaɗa kai tayi tace"yauwa yanzu kayi magana,so nake imamu Ya Auri Sameera nan ba da daɗewa ba.

Cikin Siririyar murya Abbu yace "shikenan Nana abunda kike so shi za'ayi".

Washe baki tayi ta dafa Sameera dake ji kamar An sata a Aljanna tace "kinji ko sameerah dama na faɗa miki ki kwantar da hankalin ki muntari ya haifu a cikina".

"Wallahi tallahi bazan Auri Sameera ba,dana Auri Sameera gwara na mutu banyi Aure ba,wallahi bazan Aureta ba ,'dan wallahi kuka ce sai na Aureta zaku rasani, 'dan Zan mutu ne,

Wallahi Abbu bazan Auri Sameera ba sabida a yanzu maganar da ake babu macen da nakejin a duniya bana ƙauna sama da ita saboda tana neman shiga tsakanina da rayuwata da farin cikina wanda Nana ke tayata wajen ganin sun kashe ni,

Wallahi bana santa na tsaneta,

Da kuka imam Ya ƙare maganan sa Kafun Ya tashi Ya bar gurin da saurin sa ba Tare da Ya saurari kiran da suke masa ba,

Ɗakin sa Ya nufa Ya kulle dan yasan dole wani zai biyosa ,ille kuwa Ya tsinkayi muryar Usama yana Mai faɗin Ya buɗe masa .

Kallan Nana ummu tayi idanun ta a cike da kwalla Tace "ban tab'a tankawa hukuncin ki ba Nana tsawan shekara talatin da shida kenan ina Auran muktar amma ban tab'a jin daɗinki ba,Bansan menene na miki a rayuwata da kika ɗora mun karan tsana ba,ban sani ba Nana ,Allah Ya sani zuciya ɗaya nake zaune dake sannan Kallan uwa nake miki ba uwar miji ba,amma Bansan dalilin da yasa ke kike ɗaukata kamar maƙiyiyarki ba,amma duk bama wannan ba,imam mene yayi miki da kike san tsangwamawa rayuwar sa?"

Yace baya san sameerah umaimah yake so,menene aibun haka fisabililahi?

Zan yarda da komai amma bazan lamunta ba muddin wannan abun yayi sanadiyar da na rasa imam,Abbun usama ka rubuta ka aje idan wani abu Ya samu imam na gama zama da kai .

Tashi tayi ta bar gurin tana riƙe kukan da ke ƙokarin kwace mata .

Tsaki Nana tayi tace"shirman banza,dama wanene ke sanki da Muntari,Allah Ya kiyaye hanya kuma Aure ne sai anyi,

Kallan Sameera tayi tace ke tashi muje ki matsa mun ƙafata ,kai kuma muntari kaji dai abinda nace 'dan haka afara shirin biki "

Bayan tafiya Nana Affan Ya kalli Abbu wanda Ya kasa cewa komai,yace "Abbu kayi haƙuri amma kaima kasani Nana bata kyautawa ƙwataƙwata,ai baka tab'a jin ummu ta tanka mata ba sai yau,ya kamata an'a yiwa Ummu adalci ,"

Tashi yayi yabar gurin yayin da Afnan ta taimakawa intisar ta tashi suka bar gurin.

Tashi Abbu yayi ya nufi ɗakin Ummu,a buɗe Ya tarar dashi 'dan haka Ya murɗa handle ɗin Ya shiga,

Zaune Ya tarar da ita tana kuka,zama yayi gefenta Ya jawo ta jikinsa yana Mai shafa mata kanta a hankali,gudun kukanta ta kara Har da shesheƙa,

A hankali cikin kwantar da murya ta sigar lallashi yace "idan kika rabu dani nayi yaya nikuma?"

Bana san na kuma ji kince zaki rabu dani 'dan idan na rasaki Zan shiga cikin wani halin,

Raba jikinta tayi da nasa tace"Abbu haka imam zaiji idan Aka rabashi da Umaimah,yana santa da dukkan rayuwarsa,ka taba ganin soyayya haka a idanun imam? "

A wannan karan imam ya ga wadda yake so sannan bai damu da past ɗinta ba so mene damuwarmu?

Kamo hannunsa tayi tace "ɗan Allah Abbu kar ka bari Nana ta tarwatsawa Imam rayuwarsa ,Zan iya shanye komai na Nana kayi haƙuri amma banda wannan."

Murmushi yayi yace"bana san ganin hawayenki abar ƙaunata ,hawayenki nasani cikin damuwa,sannan na miki Alƙawari zan san duk yarda zanyi imam Ya samu abunda yake so."Hannu yasa yana Mai goge mata hawayen inda cikin yarda da maganar sa tace "nasan kana cika mun Alƙwari 'dan Allah ka cika min wannan,ni nasani umaimah ba yarinyar banza bace ita tata ƙaddarar ta haka tazo mata kilan Auran imam Shine cinyewar jarabawarta,idan akan Intisar ko Afnan Ya faru na tabbata bazaku tab'a cewa wane baiyyi su Auresa ba,".

Hannu yasa akan lips ɗinta yace "shhhh,ki bar magana da kukan nan honey imam zai Auri umaimah,Bansan taya Zan fara da Nana ba amma koma menene Zan shawo kanta sannan Auren imam da umaimah kamar anyine insha Allah,!

Cike da murna ta faɗa jikin sa tana Mai faɗin nagode mijina Allah Ya barmu tare Ya raya mana zuri'ar mu.

Kissing kanta yayi yace"ameen masoyiyar muntarin Nana".

Ƙaramar dariya tasa tana Mai jin san mijinta har ranta.

****************************

Washe gari Umaima tayi ta zuba idanu tana Mai san ganin zuwan paki amma shiru,sukuku haka take abubuwa cos a yanzu ganin sa ya zamar mata cima,

Da kyar ta iya maida hankali wajen ganin patients' a consulting room,

Har lokacin lunch paki bai zo ba and babu KB ballantana ta tambayeshi gashi bata da numbernsa,sannan koda ta kira wayarsa a kashe take,

Message ta tura masa akan idan yaga saƙon ta Ya ƙirata,

Tana zaune bayan ta idar da sallah taji ana mata Knocking,

Izini ta bayar da a shigo,

KB ne ,cikin danne damuwarta tace "yes and hope abokinka lafiya baizo aikiba,.

Ɗan karamun murmushi yayi yace kinyi baƙone ma,

Baƙo?

Ta tambaya tana mai juya wanene zai zo gurinta yau?

Izini ta bashi akan yaje Ya shigo dashi.

A fizge ta kalle sa tana Mai mayar da wasu files cikin locker tace"sai yanzu kaga daman zuwa kenan i thought Ai day one of us being official har ka manta dani paki".

Zama yayi kan kujerar da yake facing ɗinta yace "Paki ne ,amma usama paki ba imam paki ba,"

Da sauri ta ɗago jin ba miryansa ba amma Mai Kama da tasa sannan mamallakin muryar Mai mutuƙar kama dashi sai dai wannan yafishi shekaru wanda hakan Ya tabbatar mata yayan sa ne!

Da sauri tace"im sorry nazata imam ne,sannu da zuwa,ina wuni".

Murmushi yayi wanda Ya sake fito da kamarsa da imam yace"sunana usama Paki sannan ni yayan imam ne,ni yake bi a gidan mu,tabbas yanzu na gane dalilin da yasa imam haukacewa akan mace ashe dai macen ta kai har ta kai da saboda ita Ya gudu daga gida.

Cikin tsantsar damuwa tace"Ya gudu daga gida?"Saboda mene?

Murmushinsa Ya kuma faɗaɗawa ganin yarda lokaci ɗaya ta ruɗe yace"ki kwantar da hankalin ki yana yiwa soyayyar ku yaƙine and na tabbata shike da nasara,Nana ce tasashi gaba,Sorry kilan baki waye ta ba ƙaƙarmu ce".

Yar ƙaramar dariya umaimah tayi ta nuna masa hannunta inda Nana ta Cije ta tace "kaga shaidar Nana a jikina ,she bite me".

Buɗe baki yayi kafun yasa dariya yace "Nana and her wahala God mai Ya haɗa ku,labari ta fara bashi abun yana Mai dawo mata sabo yana sata dariya cos tsohuwar nan sai Allah".

Kamar sun saba da juna idan ka gansu,

Ban ko sa an kawo maka coffee ko tea ba ko wani drinks.

Saurin ɗaga mata hannu yayi yace "no"kafun Ya kalli agogon Hannun sa yace "zan wuce lagos yau ne nace bari nazo na ganki muyi magana,"

Nasan kina da past amma past ɗinki ba zai tab'a lalata soyayyarki da imam ba sabida nasan yana mutuwar sanki and a idanunki Kema nasan haka,

A yarda imam ke sanki ina roƙanki ki riƙemun kanina amana ,nasan kinfisa sanin rayuwa cos you've been through alot,and ina tare daku a koda yaushe,.

Cikin jin nauyin sa tace "ina yaje hamma"

Cikin jin daɗin girmamasan da tayi yace"kar ki faɗawa kowa ,yana Airport' yana jirana zamu bi jirgin yamma mu gudu lagos na ɗan boyesa yayi kwana biyu Kafun Ya dawo ,kiyi masa cover ,"

Murmushi tayi tace"Allah Ya tsare hanya Hamma."

Sallama yayi mata Ya tafi a yayin da take shirya fushi da paki muddin bai nemeta ba.

A/N

Wane ke jin kamar Ya zane Nana bayan ni?🙄

Chuchujay ✍🏽

Tbc

https://whatsapp.com/channel/0029Va9RLKT2P59fHSa7Ia1j

Join My whatsapp channel inda Zan baku noorurrahman kyauta.

Yes paid novel ne amma Zan baku shi a channel ɗina kyauta,

Just follow and share i want audience domin baku,

Share it make it go viral
[11/25, 9:42 PM] CHUCHUJAY✍: AURE UKU

(a hospital romance)

By

Chuchujay

Episode 1️⃣2️⃣

Nana Mai kike faɗa haka ne ?

Kin 'fa san wannan maganar babbar magana ce!

Kallan sa tayi tana Mai gyatso baki tace "yo muntari kace na masa sharri mana kawai!"

Riyal Aini na kalli bidiyan sa da wannan shegiyar guzumar likitar suna Alfasha,

"'dan ma ina tsoran idona kar Ya lalace shi Ya hanani cigaba da kallo amma wallahi imamu ne,"

"Ina faɗa maku neman mata Ya hana yaran nan Aure ko rashin lapia to ashe kalau mazantakar sa take zina yasa a gaba Ai wallahi imamu yaji haushin rayuwar sa Ya bata wayansa"

"Kallanta ta mayar kan ummu wadda tayi jugun tana Kallan Nana ,cikin haushin ta tace "Ai habiba baki gama tagumi ba sai Yar iskar ta kawo ciki tace nasa ne".

"Dama ni na dade da sanin baki da tarbiyar da zaki bawa yara,yanzu wa gari yawaya?"

Da Ya tashi dai bai bi munanniya ba amma fa akwai raini da taƙama.

"Shi yasa da na kama fatarta sai a na ga jini,"

Cizanta kikayi Nana?

Abbi Ya tambaya da mamaki karara a fuskarsa .

"Yo kar na Cije ta ,Ai wallahi muntari idan ka kasa saka yaran ka sukawa yarinyar nan jagajaga a cikin garin nan baka haifu cikina ba,"

Tunda shi ɗan ka Ya kasa Ya tsaya zoƙoƙo yana kalla tana mun zagi na Inna naha ya kasa cewa komai kai ka yo gaba ka ɗauki mataki.

"Ni ban san ma Mai yarinya irinta take yi a gurin cetan rai ba ,baka ga idanunta ba fiƙi fiƙi kana kallo ansha kwanan gidan maza,"

Ƙishin ɗin ma da naji gurin sameerah yarinyar nan yar Albarka wai tana da ƴara uku kuma ko wannan su a Aure guda ta samu .

"Ni ban ma yarda ba ,kar kaci mamaki Shegu ne".

Kuka kuma ta fashe dashi tana faɗin "wallahi muntari tunda uwata ta haifeni ba'a taba zagina fes kamar yarda ƴar nan ta zageni ba,

Har da kirana karya."

"Cikin damuwa irin ta ɗa idan anyiwa mahaifiyarsa Abu mara kyau Abbi yace"kiyi shiru Nana dole za'a mata hukunci ,Kin manta wanene ɗan ki ?"

Wanene ubanta ?

Idan hukuncin ya kama har shi.

"Matse kwalla tayi tace Ko BULAMA ko menene,naji dai ana faɗin dai babanta na da kuɗi wanda nasan duk kuɗin sa bazai Kai Ka ba"

"Ba dai ɗiyar Alhaji Usman Bulama bace ,ɗiyar sa kwaya daya tilo".

"Jan majina Nana tayi tace "yo idan ma itace menene abun mamaki?"

Amma gaskiya bana tunanin itace wannan daga ita har ubanta yan iskane tunda Ya haifo Yar iska take bi layi layi tana lalata mana yara.

Ummu ce a karo na farko tace "Abbi kar mu faɗa conclusion akan abunda bamu da tabbas".

Cikin balai Nana tace "conculosho,kar ki fara mana ƙaryar turanci anan 'dan Kinganki kinzo daga kasar su,"Nan muntari sai da yaga ƙarshe biro ,

Kar ki fara dani yanzu na sauke miki abinda Ya dameni dama baki san irin haushin ki da nake ji ba.

Abbi zai sake magana sukaji muryar Paki a falon ƙasa yana zuba jaraba,

A tare ko wanne ya miƙe 'dan zuwa ganin wainar da ake toyawa.

A falon suka tarar da imam yana jan akwatin sameera yana Mai faɗin"i warned you Ai,amma duk zagin da kikaje asibiti kika yiwa umaimah bai ishe ki ba sai da kika saka Nana cikin haukanki,"Kizo ki wuce inda kika fito tunda banga abunda kike anan ba karshe ma dana tuna baki da alaƙa da kowa a Gidan nan sai ni.

"Ni kuma a yau na datse dukkan alaƙar dake tsakanina dake dama Ai saboda ni kike samun darajar zama a anan ɗin idan ta kama".

Tsawa Abbi Ya saka masa ganin yarda yarda yake jan akwatin Sameera tana binsa tana faɗin yayi hakuri.

"Tsayawa yayi jin Faɗan da Abbi yake na uban me yake haka".

"Juyowa yayi yace "nasan duk abunda ,yake faruwa Nana ta sanar daku ,amma Abbi duk abinda Nana ta sanar da kai ba haka bane ."

"Cike da jaraba Nana tace "kawai fito fili ka kirani maƙaryaci Ai ba yau ka saba ba,"

Tunda kayi Abun kunya dole ka tsaya Nan cikin rashin jin kunya ko kaɗan ana fada kana faɗa,

Kamata yayi akaika kotin musulunci a zane ka a maganar da ake,amma ina fitsararre Mai sauran jinin nasara a jikinsa .

"Amma Nana abunda kike fa kema kinsan baya kyautuwa ,Hamma imam Ya faɗa yace clip ɗin editing ne amma ke Kin dage akan gaskiya ne ,kawai ki fito fili kice dama kinaso Ya lalace"

Afnan ta faɗa tana Mai daurewa dan taji haushin Nana da sameera abunda sukayi shi yasa koda Paki yazo yace tabar gidan ta goya masa baya.

"Kana ji dai muntari Abunda ƴar ka ke faɗawa uwarka!"

Nana ta faɗa cike da san fitina.

Gyaran murya Abbi yayi yace "Imam aje mata akwatin ta kuzo baki ɗayanku ku zauna ina san magana daku."

"Ko wanne a cikin su Ya samu guri Ya zauna kowa kuma da abunda yake saƙawa a ransa".

Abbi ne Ya kalli Paki yace "imamu ka faɗa mun menene yake faruwa ,".

Gyara zama paki yayi yace "Abbi duk Abunda yake faruwa wallahi ba gaskiya bane,Abbi ka sanni sannan ni ɗanka ne da duk tsanani bazan taba Aikata zina ba,"Wallahi tallahi Abbi clip ɗin nan ba Gaskiya bane ,maganar da nake itace gaskiya sannan Abbi zuwa gobe da safe insha Allahu zan fito maku da gaskiya.

"Bansan wanene yayi ba ko dalilinsa nayin haka ,amma muddin na kama ko wanene bazai tsallake ba,."

"Sannan Abbi ina so sameera ta bar gidan nan ne Cos itace ta ɗauki Nana ta kaita har asibitin mu taje ta ciji umaimah ,

Wallahi Abbi indai kaga abunda Nana tayi a asibitin nan sai kaji kunya ,

"kafun Dr Bulama wata likita fa ta tara ta yayyankawa mari ,yanzu tana kai ƙarar Nana,shari'a sai ta haukanta,

"Haba koda Abunda ake faɗa gaskiyane Ai Nana bai kamata tayi abinda tayi ba."

"ballantana ma gaskiya ne,"Nana ta faɗa tana Mai kaɗa kafafu akan kujera.

Ai sai ki bari gobe tayi muga Mai faɗin gaskiya "Affan dake jin kamar Ya kifar da Nana Ya faɗa".

"Uban uwarka Apan,ni kake kira makaryaciya?"

Wata irin hayayyakowa Nana tayi ,

Abbi ne Ya rigata ta hanyar kai wa Affan duka ,Kafun yace tashi kabar gurin nan shashashan yaro.

Miƙewa Affan yayi,

Ɗan lankwasar da kai Nana tayi tace "Ai da baka dakesa ba muntari razanasa nayi niyar yi ,kar ka kuma kai masa duka 'dan Allah bana so".

Wani irin haushinta Ya rufe Affan,

Kaɗa kai yayi yabar gurin inda Afnan ke faman aikawa da Nana saƙon Kananun harara.

"Yar gidan wanene yarinyar?

Abbi Ya tambaya.

"Alhaji Usman Bulama".

Da mamaki Abbi yace wanda na sani dai?

Kaɗa masa kai imam yayi yace shi Abbi.

Alhaji Bulama dai da kowa Ya sani Attajirin dake living lowkey life a garin Adamawa.

Tsuru tsuru Sameera tayi 'dan bata san umaimah ɗiyar Mai kuɗi Mai numfashi haka ce ba.

Ɗan gyarawa tayi da sabon maƙirici 'dan tasan yarda Ya kuɗiri niyar sai ta bar gidan to sai ta tafi ita kuma bata zo 'dan ta tafi ba ,tazo ne 'dan ta samu paki a wannan karan.

"Ciki muryar nadama ta ƙarya tace "nasan nayi laifi imam kayi haƙuri 'dan Allah ,idan kana so ma Zanje na bata hakuri 'dan naji ance ƙarkashinta kake ba naso kuma na zama silar zama maka matsala."

Kayi haƙuri ummu ,Abbi,da,Nana kuyi hakuri.

Kallanta ta mayar Kan paki tace ,zan koma hotel ɗin kamar yarda kace paki, gobe insha Allahu zan kokari a maidani  niger naje gida nayi IT na a chan.

"Kaɗa kai Nana tayi tace"Allah sarki,bansan yaushe yaran nan zai gane soyayyar da samira ke masa ba,bari abunnan Ya mutu muzo a fara maganar Aurenku".

"Da sauri Paki yace"ni da Sammy ba soyayya muke ba Nana 'dan Allah kibar haɗa maganganu."

"Tabe baki tayi tace "Ai kuma sai kayi tayi Aurene kamar anyi."

Zai magana Abbi Ya katse ta hanyar faɗin "babu inda sameera zata je nan gidan kamar nasu ne, na yarda bata kyauta ba amma babu inda zata je,zata zauna anan har sai ranar da taga yayi mata dai dai da ta tafi.

"Zai magana ummu ta hanasa ta hanyar faɗin"imam ya isa haka ,kasan ba yau sameera ta saba zuwa nan ta zauna ba ,sameera Ai ta zama yar,gidannan,".

"Tashi yayi baice komai ba ya musu sallama amma a ƙasan zuciyarsa hakan bai masa daɗi ba 'dan yasan Sammy ba tazo da alheri ba.

"Sameera Hashim asalin gwarawan Niger minna ne ,tun secondary school take tare da KB da Imam a Federal government college Abuja,"

Tun junior class suke ture ,a lokacin sammy tayi ta shige musu har sai da ta zama ƙawarsu kuma ƙanwarsu ,sune ke shigar mata faɗa Cos a lokacin she's young ga tsoro ga tsokana,

"A haka iyayensu suna zuwan musu visiting suka san sameera wanda a haka suka saba da iyayenta aka zama kamar ɗaya,"

Baya gama makarantar su suka samu Admission tare a NILE university tare inda ita take karantan Nursing su kuma medicine ,

Sau da dama sameera kan zo Adamawa kawai dan imam wanda dama tun suna secondary school ta fada masa tana sanashi amma shi Ya nuna mata a ƙanwa Ya ɗauketa,

Iyayanta sun yarda da iyayen paki ɗan har ziyartar juna sukanyi sabida amintakar da ta shiga tsakaninsu dan haka duk lokacin da Sammy tace zata Adamawa basu hanata,

"Ko a yanzu ma intern ɗin da tazo babu yarda iyayenta basuyi ba akan tayi a nan minna amma ta kafe ",su kuma iyayenta irin mutanennan ne da basu yawan kwab'ar ƴaƴansu a duk Abunda suka so Mai kyau da mara kyau,kawai buƙatarsu  ta biya.

***********

"Kallan umaimah da ta baro ɗakin daddy Hindu tayi tace "girl Ya dai?"

Ƙaramun yake umaimah tayi tace "daddy is on it he's getting it investigated amma for now an gano location ɗin da aka saka clip ɗin,   "Anan asibiti ne,im just wondering wanda yayi sannan Mai na masa?

Dafata Hindu tayi tace "ki kwantar da Hankalinki komai zai zo Ya wuce,and about paki yarda kikayi treating ɗinsa bai yi ba."

"Ɗan shiru tayi tana Mai tuno irin halin da Ya shiga,hes young sannan yanzu yake fighting ma career ɗinsa,"Ita kuwa duk wani abu da take mafarkin achieving tayi,sannan idan ta bar CITY hospital akwai asibitocin da dama da zasu ɗauketa,dole She will fight this for him.

"Karshe ma a yanzu da blue print na asibitinta da zata buɗe sannan gini Ya ɗauki nisa ,so take Ya zamana ta gina katafaren asibitin da za'ayi alfahari da And ta tabbatar idan komai ya tafi mata dai dai hakan za'ayi."

"Snapping yatsa Hindu ta mata tace girl are you 'in Love."

"Da saurinta tace uwar Love ba Love ba".

Dariya suka saka a tare kafin ta kalli Hindu tace "it been a l'ong time ".

Hope ziyarar nan da kika kawo mun zaki kwana biyu sannan no hotel a nan zaki zauna.

Murmushi Hindu tayi tana ɗaga hannu 'in surrender tace naji but maganan bina misra bai tashi ba dole ki zauna kiyi facing aikinki you're needed there girl.

Indai kuma ba aiki zaki dawo Cleopatra Hospital  ba wanda zan murnar haka ,.and guess what

nayi saurayi balarabe sunansa Ahmad ,soon zan kawo shi kasar nan yaganku dangina Da kuka rage anan Cos Ya gama siye ummi a kasar nan.

Dariya suka sa suka cigaba da hirar yaushe gamo har yara suka dawo.

*******

Okay im still having test tomorrow but still tho.

Trust me ,ina mutuƙar sanku

Zaku cigaba da samun Double update ne kawai idan na gama test.

School is stressing me for now

Follow me on wattpad And arewa books @chuchujay

https://www.facebook.com/groups/805959663295457/?ref=share

Xx

Chuchujay ✍🏾

Tbc

[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU

(a hospital romance )

By chuchujay

wattpad :@chuchujay

https://whatsapp.com/channel/0029Va9RLKT2P59fHSa7Ia1j

Join My whatsapp channel inda Zan baku noorurrahman kyauta.

Yes paid novel ne amma Zan baku shi a channel ɗina kyauta,

Just follow and share i want audience domin baku.

Episode2️⃣5️⃣➡2️⃣6️⃣.

Baki ɗaya haka nan Umaimah ta karasa ranarta a sukurkuce,bata san kasancewar paki a tare da ita ba Ya kamata sosai sai a yau da kwata kwata bata ji sa ba ko tagansa,

Motar yaya Abubakar da ta gani a gida Shine Ya tabbatar mata da yana gida ,

Parking motar ta tayi a gefen tasa ta nufi sashen sa kai tsaye,

Tun a ƙofa taganshi yana shirin shiga,

Yana ganin ta Ya faɗaɗa fara'ar sa yace "umaimah Kin dawo kenan,"

Murmushi tayi tace" wallahi yaya na dawo and ganin motanka yasa nazo na gaishe ka cos na kwana biyu ban ganka ba,

Shiga yayi tana biye dashi a baya,

A falo ta tarar da iyalan sa ,da gudu yaran sukazo gareta suna mata oyoyo inda mahafiyarsu ke ta mata fara'a tana Mai faɗin dama wai kina gidan nan umaimah,yaushe rabon da na saki idona?

Zama tayi tana Mai faɗin"maman sultan baza ki gane ba fitar ce da sassafe wani lokaci bana shigowa sai dare Chan,".

"Gaskiya dai Allah Ya taimaka ,aikin ku Ai sai ku,

Bari na kawo miki abinci,

Da saurinta tace "a'a Aunty Im okay dama nazo magana ne kawai da yaya Abubakar."

Ƙaramun murmushi tayi tace "bari na baku guri dan tsakanin ki da yayanki sai Allah"

Bayan tafiyarta Ya Kalleta yace "umaimah Allah yasa lafiya,"

Murmushi tayi tana Mai Wasa da hannunta tace"Yaya dama ina san magana da kai ne,ko nace

ina san na nemi shawarar ka saboda ina tsoran nayi abunda zai dameni,wasa ta cigaba dayi da hannunta Kafun tace"Yaya I've found someone ,i mean wanda yake san Ya Aureni and im not against it,

I might sound somehow amma yaya Im loving the idea saboda ive fallen for this guy,

Sannan yaya bai tab'a Aure ba and He's just a month older than me,

Shine babban abunda nake tsoro sabida abunda mutane zasu ce,wasu zasu ga kamar Im selfish ina ƙokarin jansa cikin rayuwata bayan nasan ko Aure bai tab'a yi ba,amma yaya abunda nake ji a tattare dashi ko akan Hafiz banji ba,sannan yana mun soyayyar ni kaina takan bani tsoro,

Ban san Ya zanyi ba,

Duk abunda na fuskanta a rayuwa ta a wannan karan bana ganin komai sai alaƙata dashi

Shiru Yaya Abubakar yayi bayan takai ƙarshen zancen ta Kafun yace"a ina yaran yake ,ɗan gidan wanene".?

Licking lips ɗin ta tayi tace"Yaran Admiral Muktar paki ne"

Riƙo hannun ta yayi yace kali nan umaimah,eh nasan abun sound somehow amma it doesn't matter ,nasan dole mutane zasuyi magana kamar yarda kika ce amma abu mafi muhimmanci Shine muddin idan zuciyarki ta kwanta dashi ta yarda dashi ki saurareta ,saboda you deserve some happiness Sannan yaran nan bake kika masa dole Ya soki ba ,shine yaji yana sanki kuma ya amince zaiyyi rayuwar sa dake so Allah wadai duk abunda mutane zasu faɗa.

Babban farin ciki na Anan Shine ,yarda baki  sare da Aure ba,bakice a'a ba saboda Hafiz ma Ai yazo maki da soyayya,nayi farin ciki mutuƙa da kika saka a zuciyarki ba kowane Ya zama ɗaya ba sannan da ikon Allah jikina Ya gama bani a wannan karan baza muyi dana sani ba,

Duk abunda ke saki farin ciki umaimah nima yana sani ,and a rayuwata bani da buri da Ya wuce naga kinyi settling down a gidan mijinki,abu ɗaya Ya hanani magana wanda Shine gudun yarda zaki ɗauki maganar ,amma tunda yau da kanki kike so na miki Alƙawari zan tsaya miki kamar koda yaushe,

Duk wani damuwar ki in dai ina da maganinta Zan maki,Just say the word,and kar ki damu i will talk to daddy .

Murmushi tayi tace "nagode yaya ,kai ɗan uwa na gari ne,ina jinka a zuciya ta,ina ƙaunar ka saboda ka damu da damuwata kamar ciki ɗaya muka fito ,ko iya abinda na samu a gidan nan ke nan na godewa Allah.

Gyara zaman sa yayi yace "ni dake umaimah Ai ciki ɗaya ne,ko baki san uba ɗaya ne ciki ɗaya ba?

Kar na kuma ji kince ba cikin mu ɗaya ba ,da ni dake da umar da usman da Aliyu duk cikin mu ɗaya,it doesn't matter hallayyar su a kanki amma ni nasan suna ƙaunar ki suna kaunar ki ,kawai wani abu ne Chan na banza yake tare musu nuna maki,wa kike tunanin yake samun sa'a kamar tamu?

Duk wanda Ya samu ƙanwa irin ki abun yayi alfahari da ita ne,kinsan yarda kaina yake ƙato idan naji abokai na nace wa "Ai Abubakar yayan young beautiful surgeon umaimah Bulama ne,sai kiji na kasa riƙe kaina 'dan har rawa yake kamar zai faɗi,its a real show up ".

Dariya tasa tace"yaya!!!"ɗan hira suka tab'a Kafun tayi masa sallama ta wuce ,.

Haka nan taji kamar an sauke mata dukkan wata damuwa ,ɗaura ɗamara tayi da zuciyarta wajen nunawa paki soyayyarta ,kamar yarda yayanta Ya nuna mata "Fuck the society as far as she's Happy "

Koda ta shiga sashen su Abdallah da Nadiya sunyi bacci Shatu kawai ta tarar a falo tana kallo,

Tana ganinta tace"sannu da zawa Adda,zama tayi kan kujera tana Mai cire takalmin ta Kafun tace"baki kwanta ba,

Hamma tayi tace "wallahi Adda wai ina jiran shigiwarki ne ko zaki nemu wani Abu,"

"Shatuuhh!"Idan kina jin bacci Just go to sleep ki daina cewa zaki jirani ko zan buƙaci wani abun ,Babu abinda zan buƙata ,idan ma inaso zanyi da kaina ,Ai kina ma ƙokari in kina mun haka bazan na jin daɗi ba ,kefa yar uwata ce ba yar Aikina ba,

Please!

Murmushi tayi tace "kiyi haƙuri Adda ,a rayuwa ta kullum burina bai wuce naga na kyautata maki ba,kin san a yan uwan mu kece mace ta farko data fara ɗauka na ta jani jiki cos kowa maganar sa ɗaya ni nayi sanadin mutuwar shifaɗo ,bani da sa'a ,kowa yaki zuwa Ya nemi Aurena kamar wata Mai kanjamau,shiyasa a rayuwata yanzu Kin bani abunyi ,cos kula dasu nadiya ina jinsa har raina ina kaunar yin hakan,suna mutuƙar bani farin ciki.

Kallanta umaimah tayi taga yarda tayi bul bul ta ƙara kyau ,Dafata tayi tace"shatuh i want the best For you sannan na ɗaukeki badan wani abu ba ace ma saboda Aikina and su nadiya na bukatar wani,amma nima ina bukatar ki kusa dani,and insha Allahu zaki gani ,sai na maki Auren kece raini ,Auren da masu yan gutsiri tsoma akan ki zasu ji kunya,"And yanzu ma maganar da nake miki na sama miki Niva open university kina gida zakiyi karatun ki,exam kawai zai kaiki,

So insha Allahu monday bana komai zan dauke ki muje muyi komai,.

Cike da murna ta rungume ta tace "nagode sosai Adda ,Allah ubangiji Ya faranta miki Ya shira maki yaranki."

Shafa kanta tayi tace ameen ya rabbi,

Wanka tayi bayan ta shiga ɗaki taci abinci ta jawo system ɗinta tana ɗan wani research ,a hankali takan duba wayarta taga koda saƙon paki ne Amma shiru,kamar ta sake ƙiran sa amma tayi ƙokari ta danne zuciyarta gudun kar ta bada kanta,

A hakan nan ta gama abunda Zatayi ta kwanta amma tunanin ta baki ɗaya Ya karkata kan paki ,bacci b'arawo ne kawai Ya ɗauke ta tana Ayyana yarda yake.

Washe gari kasancewar bazata Aiki ba yasa ta joining yan gidan breakfast duk da kuwa yaya usman da umar sun fita,

Bayan sun gama cin abinci tana ƙoƙarin tashi daddy yace "umaimah ina san magana dake mai muhimmanci ,kizo sashena,,"

"Maganar baza'a iya yinta bane a cikin mu sai anje sashen ka Alhaji?"

Maganace dai ta budurwar zuciya da ɗiyar ka take da ita sannan baki ɗaya bata san ta tsufa ba dan haka zuciyarta take mata kwaɗayin Abunda yafi karfin ta,Ai naji jita jitar sannan wayar da kayi jiya ta tabbatar mun ba jita jita bane.

Hajiya ta faɗa tana Mai ƙora tea ɗin ta,

Ƙaramar dariya Aliyu yayi yace "Ai ni umaimah ban tab'a sanin kina da san zuciya haka ba sai yau,ina ke ina yaran Admiral muktar ,dama dai ace babban ne ya iya maneji dake amma wanda bai taba Aure ba kuma tsaranki Ai Kema kinsani ba sai an faɗa maki ba ,san zuciyarki a fili yake sannan duk wanda yajiki yasan desperation ne ke damun ki kwana nawa aka gama

yawo da sex clip ɗin ku a duniya sannan yanzu wata maganar Aure ta bayyana . "

"Ai baka san wani abu ba Ali,ita dama sa'a ba ga kowa take ba,ka kalli umaimah a gurin nan ,bazan boye maka ba tafi kowa sa'a a yaran daddy ,i mean ka duba rayuwarta da kyau, a wannan karan ma sai gashi Allah ya kara buda mata sa'arta ta samu mutum irin imam paki,ba san zuciya bane ,rahmace ta ubangiji,Ya kamata ace ka gane hakan,

Yaya Abubakar ya faɗa kamar ba shi Ya faɗa ba cos abincin sa ya cigaba daci calmly.

Tsaki Hajiya tayi tace "kaji haushi Abubakar Ai ,indai akan umaimah ne  nana Surbajo Kafun ta tafi ta barbaɗa maka "

Dukan dining table ɗin da daddy yayi ne yasa ta saurin yin shiru,nunata yayi da yatsa yace "na faɗa maki ba sau daya ba ,ba biyu ba akan ki daina saka Surbajo a haukan ki amma baki ji ko?

Zamu samu matsala fa,ki kiyaye sannan kai kuna Ali da kake faɗin san zuciya kaima kaso zuciyar ka haifu,.

Kai daddy !!

Matar yaya Ali ta faɗa a karo na farko tunda aka fara abin 'dan tun gargaɗin daddy babu wadda tayi gigin sake shiga shirgin umaimah ballantana yaran ta,

Tashi daddy yayi yace umaimah oya ,

Babu musu ta mara masa,

Zama yayi yace zauna umaimah ,

Babu musu ta zauna tana Mai narenare da ido 'dan abinda Ya faru a wajen Ya ɗan tabata,wai ace danginka ne ke adawa da kai.

Cikin sakin fuska yace "umaimahn daddy menene baki faɗa mun ba?"

Shiru tayi ba tace komai ba ,kallon idanun ta yayi yaga sun ciko da kwalla,

Ajiyan zuciya yayi yace "kalli nan umaimah im not against duk wani abu da kika zab'a kuma kika ji a ranki Ya miki,Just go for it koda zai maki zafi daga baya, at least Ya saki farin ciki daga farko".

Daddy bama zai sani baƙin ciki ba,kamun addu'a ,na zab'i Paki and wallahi daddy ba san zuciya bane ,abunda zuciya ta ke so ne sannan ban amince da zab'in ba sai da na tabbata da hankali na Ya kwanta,and daddy inaji a jikina he's not like Hafiz ,'dan Allah daddy support me i want this.

Shiru yayi yana karantar yanayin ta,tabbas Umaimah ta tafi akan wannan yaran da bai sani ba dan ko magan nan bai kai mata ba amma ta kare,cikin san jawo da hankalin ta garesa yace "umaimah bai tab'a Aure bafa.sannan ke Kin tab'a Aure,yaranki uku fa,."

Cike da kwarin gwiwar da bata san tana dashi ba tace "daddy Annabi Muhammad (SAW)Nana khadija ya fara Aura kuma she's even older ,daddy anan ma ban girmi Paki ba,babu inda addini Ya haramta Aurena dashi,"Daddy please kaine kawai kwarin gwiwata and jikina yana bani imam alheri ne a rayuwata,

Ta karasa maganar tana Mai nare nare da ido.

Ajiyan zuciya yayi mussaman ganin Yarda umaimah ta fito masa a mutum,tabbas soyayyar ta rufe mata ido,sannan shi he's looking out for her,baya san tazo Ya yaudareta kamar Hafiz amma ganin yarda bataji nauyinsa ba yasa shi cewa"shikenan princess ɗin daddy,duk abunda kika zab'a nima ina tare dashi sannan ina Addu'ar Allah yasa Shine zai rufeki ko ki rufesa,"Jiya mahaifin sa ya kirani yamun maganar so i thought kawai irin random mutane ne musamman scammers shi yasa ban tsaya jin sa ba nace masa wrong Number ,amma yanzu tunda naji ta bakin ki zan kirasa a sa rana mu haɗu ayi magana sannan ina san ganawa da shi yaran.

Cikin kasa da kai tace"daddy sunan sa Imam",

Dariya yasa yace jaira"to imam",

Haka suka cigaba da zantawa tsakanin ɗiyar da tayi shaƙuwa Mai tsanani da mahaifinta .

************

Su umaimah an kamu 'fa,😂oh ba kunya.

Bakina da goro.

Chuchujay ✍🏾

TBC.
[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU

(a hospital romance )

By chuchujay

wattpad :@chuchujay

https://whatsapp.com/channel/0029Va9RLKT2P59fHSa7Ia1j

Join My whatsapp channel inda Zan baku noorurrahman kyauta.

Yes paid novel ne amma Zan baku shi a channel ɗina kyauta,

Just follow and share i want audience domin baku.

Episode 2️⃣7️⃣➡️2️⃣8️⃣

BAYAN SATI UKU.

Iyaye sun zauna sun gana har maganar Aure ta shiga tsakani bayan dogon binciken da daddy yayi amma har a wannan stage ɗin umaimah bata sa Paki a ido ba haka zalika muryar sa,da fari ta damu ainun amma da daddy Ya sanar da ita sun gana da shi sai ta debesa ta watsar,

Ko da gan gan bata tambayi kb inda yake ba duk da kuwa yarda zuciyata ke san sanin dalilin da yasa bai neme ta ba,bata san yi masa alƙalanci shi yasa kawai ta watsar dashi duk lokacin da yaji yayi masa dai dai yazo inda take yazo.

Baki ɗaya yaran murna kawai suke za'aje kaiwa Nameer ziyara a makaranta,

Da gudu nadiya ta shigo ɗakinta kanta ɗauke da purple ɗin headband tace "mami ki kalli band ɗin nan tayi da kayan jikina ,bana san naje school ɗin su hamma na bashi kunya a cikin frnds ɗin sa ace kanwar sa bata iya dressing ba,"

Kallan Baby purple ɗin gown ɗin dake jikinta samfarin Fendi tayi Kafun tayi mata alamu da

hannu tace"you look amazing princess ,"

Blushing tayi tace "i love You mami,"

Da hanzarinta ta fita tana Mai faɗin,Aunty Aunty ina heels ɗina,

Kaɗa kai tayi tace "Nadiya and her iyayi sai ita,"Ƙarasa shiryawan ta tayi cikin Simple but expensive ash jallabiyan ta ,gyara zaman minI veil ɗinta tayi Kafun ta ɗan yi touching fuskanta kana ta jawo flat ash and black D&G takalminta ta saka tana Mai jin zumuɗin san zuwa taga Nameer cos tayi kewarsa sosai,a hakan ma wai 'dan suna waya,

A falo ta tarar da shatuh wadda itama taci nata gayun gefenta kuma Abdallah wanda ke ta faman san gyara butterfly tie ɗin sa,

Tsigunnawa tayi ta Kama ta gyara masa kafin tace "there you go your highness",

Kissing gefen kumatun ta yayi yace"thank you my Queen."

Dariya shatuh dake gefensa tayi ganin yarda yaci magani kamar bashine yayi abunda yayi ba,

Abdallah da halayyar sa ,idan yayi maka wani abin sai ka sake dubawa kace wannan shekarar sa nawa.

****************

NIGERIAN TURKISH INTERNATIONAL COLLEGE ABUJA.

Idan ka kalli AHALIN umaimah sai abun Ya baka sha'awa duk da kuwa da sultana wadda ita kadai ta samu zuwa amma sai ta saje dasu kamar ita ta haifo su,

A hankali suke takawa zuwa inda aka tanada domin iyayen yara ranar visiting ,

Tun daga nesa Nameer Ya hango su,da gudu Ya ƙaraso gare su, Kafun umaimah tayi aune Ya ɗane yana Mai faɗin mamiiiiii,

Rungumesa tayi a jikinta jin yarda Ya ƙanƙameta cike da murnar ganin ta,

Nadiya dake gefe ne tayi gyaran murya tana Mai gyara kitsanta da Ya zubo ta ƙasan band dinta tace "hala baka ganni ba brother,"

Sakin umaimah yayi yace"come her naughty little Sis,"

Uhummm

Cewan Abdallah,

Alamu yayi masa da hannu akan shima yazo yayin da suka saka dariya,

Sulatana ma dake gefe ganin Abinda sukayi itama sai ta faɗa jikinsu tana cewa nima hamma Nameer nayi kewarka sosai.

Nikam da baibi ta kaina ba Ai ban shishshigi ba,shatuh ta faɗa tana Mai turo bakin Wasa,

Ciresu yayi baki ɗaya a jikin sa yace"oh favourite Aunty mana ,kinsan namafi kewanki akan mami,"

Dariya tayi tace "shiyasa da ka fito ni ka fara rungumewa ba Mami ba."

Rayuwar school ɗin su nameer sai dai kace kayi kewar yan gida ba wai kace kayi kewar abinda kake so a gida ba,after all kuɗin ka shagalinka,

Murna kawai da farin ciki nameer yake musamman da ya kai umaimah ɗakin su dake na mutum huɗu yace "mami ki kalla bunk ɗina,"

Yarda yake ta farin ciki Shine Ya kara tabbatar wa da umaimah batayi wrong decision ba wajen kawo Nameer nan.

"Hamma kam ina roommates ɗinka ni banga ko ɗaya ba,

Nadiya ta faɗa tana mai waige waige,

Dafa kafaɗarta yayi yace "little princess sunje tarar parents ɗin su ni ne lucky one cikin su da kuka zo da wuri,

Dan far tayi da ido cike da iyayi tace "that's how much we love You".

Kaɗa kai umaimah tayi tana Mai hango girman Nadiya,tasan dole akwai rikici dan iyayin cikin nadiya sai Allah,

Bayan sun fita suna zaune suna hira suna ciye ciyen su Nameer nata faman basu labarin

school,

Kamar a mafarki Umaimah ta tsinci muryar sa ,sallama yayi hannun sa ɗauke da ledoji manya guda biyu,zama yayi a gefen Nameer yana Mai facing Umaimah yace "da kyar na gano ku,"

Uncle Handsome?

Nadiya ta faɗa da mamakin ganin sa,

Murmushi yayi yana mai mata Alama da tazo ,da saurin ta kuwa tazo tace"nazata mafarki nake ,"Dariya shatuh tasa Kaɗan jin kini binin Nadiya Kafun ta gaida sa inda Ya amsa mata cikin sakewa sosai,

Abdallah dake gefen umaimah ma da saurin sa Ya taso ganin Nadiya ta ɗane cinyan sa ta zauna yace "sister thats my spot.

Dariya PAKI yasa ya rungumesa jikin sa yace"your Royal highness ,.

Giggling Abdallah yayi dan yana jin daɗi yaji Ya kirasa da hakan,alama yayiwa sultana da tazo su gaisa ,itama cike da ɗauki taje garesa.

Good afternoon uncle"Nameer Ya faɗa babu yabo babu fallasa,"

Murmushi Paki yayi yace "Big boy ,afternoon ,Ya school,"

Ɗan ƙaramin murmushin yaƙe Nameer yayi yace "Alhamdulillah."

Kaɗa Mai Paki yayi yana Mai san jan hirar tasa da Nameer yace "I had to fly daga lagos nazo na kawo maka ziyara,and i was thinking of abinda kake so ban sani ba cos kaƙi bari na sani so na siyan maka abunda nake so which nasan muna da same taste ne".

Sake Wani murmushi Nameer yayi yace "nagode Uncle Allah Ya kara Arziƙi,"

Ya gajiyan ka kuma na wanchan ranar da kazo,

Wani daɗi yaji a ransa dan yasan yanzu Ya fara jawo Nameer team ɗinsa.

Ba wani gajiya big boy,it was nice cos nazo naganka ma maminka.

Satar Kallan umaimah yayi wadda baki ɗaya ta mayar da hankalinta kan wayarta tun zuwan sa,

Tunda ta ɗan saci kallansa taga ya sake wani irin mata kyau da kwarjini ta ɗauke kanta,wato ma He's 'in a Good shape amma Ya maida ta kamar wadda Babu ita,

And bama gurin ta yayi niyan zuwa ba tunda Ai ya iya tasowa daga lagos yazo yaga Nameer and bama wannan ne na farko ba ,yazo Nameer ɗin kuma bai faɗa mata ba,

Lallai Paki.

Cikin sanyin murya yace "ranki ya daɗe ina wuni"

Yi tayi kamar bata san bolar da ta kwaso sa ba,

"Mami dake uncle handsome yake "

Ɗauke idanun ta tayi daga kan waya tace "Nadiya ki kiyayeni 'fa ,Kin fini kunne ne?"

Jin haka yasa shatuh fahimtar akwai wata a kasa 'dan haka tace "Nameer muje ka nuna mana basket ball field Ɗinku mana"

Da sauri nadiya ta miƙe tace "yes please Bros,nima ina san na gani,Bayan tashin yaran ta ƙara haɗe ranta ,

Matsowa Ya farayi inda take yana puppy eyes"dagowa tayi ta kallesa tace "Paki don't dare me saboda you wont like me a bit,

Hannayen sa yasa a kunne sa yana Mai yin puppy eyes yace "im Sorry baby".

Cikin jin haushin sa tace don't baby me',as 'in kama maidani wadda Bansan abunda nake ba,

3 weeks 'fa,Paki ,ka mayar dani wadda Bansan san Mai nake ba,maganar Aure ke tsakanina da kai ,you met My father ,at least ko baka neme ni ba a phone call is okay,

No koda message ne,amma gani shara,ko tafiyar ka ban sani ba ,da ace hamma bai zo ba dan bazan ma san ka yi tafiya ba,kasan mene paki?

Just Forget about maganar Aure na da kai idan har ka shirya dauka ta serious ayi maganan amma yanzu let me even warn you,stay away from me.

Cike da fushin da baisan tana dashi ba ta kare zancenta idanun ta a gefe,

Ƙara matsowa kusa da ita yayi yace "im Sorry baby im very very Sorry ,kiyi haƙuri dan Allah and ki daina cewa ban ɗauke ki da muhimmanci ba,ke ce first priority ɗina

,yes na yarda ban kyauta ba da ban kira ki ba sannan banzo na faɗa maki zanbi hamma lagos ba,but honey im hand tie ,Nana was on My neck,ga sameerah,dole na kashe wayana and zuwan da nayi naga daddy i waited for you baki zo ba,

And bana san zuwa asibiti saboda kar asan nazo,i was fighting for us, tafiya ta ɗinnan ne kawai yasa Nana bata cigaba da takurawa ɗin nan da maganar Auren sameera ,

And lastly i fall ill.

Da saurinta ta ɗago ta kalle sa cike da damuwa tace ill?

Fuskewa ta sake yi da ta fahimci damuwarta tace"that still doesn't justify your actions paki,im angry ".

Juyar da kanta tayi,

Sake dawowa gabanta yayi yace dan Allah Abar ƙauna kiyi haƙuri ,duk yarda zan faɗa maki bazaki gane ba amma rashin jin muryarki da banyi ba cikin satin Allah kaɗai yasan irin damuwar da na shiga wallahi,

Dan Allah kiyi mun Afuwa bazan ƙara ba,and guess what? tafiyana cewa Nana akai ina Chan asibiti a kwance ban san inda kaina yake ba sannan ciwan sanki Ya ke san kashe ni,

Dariya yasa yace "da ƙyar ta haƙura amma da sharaɗin a gidan mu zamu zauna a part din da daddy ya gina kwanan nan zamu zauna nasan she Means trouble amma we have no option dole mu bi nata ko na kwanaki Kaɗan ne,

Im sorry baby im so selfish idan yazo kanki ,ina san ki kasance tawa ko yaya ne,dan Allah durlyn let me be the one for you,lets fight this together,

Yarda yayi da ido kamar zai kuka ta kalla.

Tashi tsaye tayi tace "ka sake practicing  essay ɗin nan idan kaje inda nake a adamawa. "

Chuchujay ✍🏾

Tbc.

[11/25, 12:19 AM] CHUCHUJAY✍️: AURE UKU

(a hospital romance )

By chuchujay

wattpad :@chuchujay

https://whatsapp.com/channel/0029Va9RLKT2P59fHSa7Ia1j

Join My whatsapp channel inda Zan baku noorurrahman kyauta.

Yes paid novel ne amma Zan baku shi a channel ɗina kyauta,

Just follow and share i want audience domin baku.

Episode 2️⃣9️⃣➡️3️⃣0️⃣

FRIDAY 12:00pm

Tun daga harabar gidan Bulama zaka san ana gagarumun taro,

Idan ka tsaya Kallan babban compound ɗin wanda aka ware gefe aka tsantsarasa cikin yanayi na event zaka ce wani arnen hall ne aka kama 'dan gurin Ya tsaru ciki tsaruwa da decoration na blue and white,

Gurin da amarya zata zauna kan sa abun kallo ne,

Biki ne ake na kwana ɗaya wanda duk wanda Ya hallarce sa zai daɗe yana tuna wannan biki,

(Da Alƙalami na da littafina na taka 'dan shiga cikin gidan Bulama dan ɗaiɗai kun mutanen da nake gani basu gamsar dani ba ,mutum ɗaya nake san na saka a idanu na wato Umaimah Bulama ,sannan ina san na tsinci labarin shin bikin wa ake gidan attajiri bulama).

Ahalin gidan maza da yan uwa da sukazo baki dayan su shirye suke cikin rich white expensive getzner a yayin da bakin daddy kuwa yaƙi ruruwa,

Fita sukayi harabar gidan suna masu hawa Arnan motocin da suka mallaka domin isa baban masallacin Sudais ƙashim domin gabatar da sallar juma'a da kuma ɗaurin Auren da zai kwashi Alumma masu numfashi After All ɗaurin Aure ne za'ayi na ɗiyar Bulama tilo,wadda take tsoka ɗaya a miya garesa,A karo na HUƊU.

Magana ta mutane dama baka isa ka tare ta ba muddin idan sukaso yin ta,haka nan maganar Auren Paki da Umaimah ta ringa yawo a duniya kamar bonfire,ko wanne vlog da gossip page idan kaje maganar su Ake,wasu suyi Negative magana wasu positive Har da masu faɗin umaimah ta Auri ƙaninta,wasu suce asiri tayi masa ta Aure sa,wasu suce Auren kuɗi ne da dai sauran su,sun gagara gane soyayyar dake tsakanin su,

A watan da aka saka na bikin su ba karamar soyayya suke nunawa juna ba ,kar ma ace paki wanda baki ɗaya yarda take amsa masa soyayyar sa yasa shi kara zaucewa a soyayyarta ,

Wani lokacin har kunya yake bata a asibiti yarda yake zaƙewa soyayyarta ,tun ana gulmar har An haƙura saboda basu bawa maganganun mutane attention ba ,love ɗinsu kawai suka saka a gaba .

Maganar Auren su ba a wani saka ta da nesa ba saboda yazo Aure kuma ko wanne side sun amince sannan Ita ba budurwa bace da za'a tsaya wani bata lokaci,dan haka iyayensu suka taƙaice lokaci da yardar su,

Hajiya Nana kuwa kowa yayi mamakin yarda tayi shiru ta kwantar da hankalin ta kamar dama tun farko ba ta ƙi Auren ba,

Babu wanda Ya maida hankali sa gareta dan kowa Ya saka shi ne as ta haƙura sannan tasan rigima ne kawai ta saka a gaban ta.

***

Zaune Umaimah take bakin mirror tana gyara gelling gefen sumarta da tasha kananun kitso wanda suka zuba bayan ta kasancewar ta mace mai yawaitar suma,

Tsantsaɗediyar kwalliya ce a fuskarta wadda batayi kadan ba bakuma tayi yawa ba,

Idan ka Kalle ta Zaka so ka kuma saka ta ciki Idanun ka saboda irin kyau ɗin da tayi mai ɗaukar ido,hannun ta zane da ja da baƙin lalle,Abun ka da Mai haske sai wanda Ya kalla.

Daga gefe Hindu dake ta faman gyara ring light tace"beb yau Paki bana tunanin zai iya ɗauke idanun sa akan ki ,kinga yarda kika kashe ni kuwa."

"Ƙaramar dariya tayi tace "babban show off ɗin bai wuce ace ina da ƙawa kuma yar uwa likita sannan a wani hannun make up artist,girl idan nacewa wani ke kikayi kwalliyar nan ba lallai a yarda ba fa,.

Murmushi Hindu tayi tana mai gyara gashinta  tace "sai ma Kin fada musu na tsuma ki a hamam ɗina na egypt zasu kara shan mamaki,i Just pray kar kisa ɗan mutane hauka cos i trust me .

Dariya umaimah tasa tana Mai fadin ke fa abunki sai ke Masoyiya ,ni kam Buɗar kan nan da za'abi ta tawa ma baza'ayi ba cos girl this is My fourth nikah,mene sabo a ciki

Dafata Hindu tayi tace"imam ne sabo a ciki,girl munji Auranki na Huɗu kenan but trust me jikina Ya bani this is for the best sannan insha Allahu baza kice dama Kin sani ba,cos soyayyarki a idanun imam gaskiya ce,sannan ahalin sa kowa Ya karbe ki,his mom loves you with all her heart,Just cheer up ki saki jikin ki kiyi murna da ni'imar da Allah yayi miki,cos ba kowa yake bawa wannan damar ba,

Ni yanzu ki kalleni mana turning 30 amma ko na fari banyi ba,Ai jira nake kawai a gama bikin ki mu kaiki ,ko Ahmad yaƙi ko yaso sai munyi Aure,

Dariya Umaimah tasa tace "Poor Ahmad yaga rayuwa hannun Hindu,"

Suna cikin wannan hirar ƙaran text message Ya shigo mata daga layin paki,

Murmushi tayi tai clicking dan karantawa ,

"Ina Mai tayaki murna da farin cikin zama matar Imamu Paki cos yanzu Kun zama mallakin juna,"

Murmushin da take faman yi ne yasa Hindu faɗin "An ɗaura hala",

Cike da murmushi tace "Allah yayi Hindu ,na zama matar Paki,i Just cant blv it sai kace a mafarki,"

Godiya ta ɗaga hannun ta tana Mai godewa Allah ,

Guɗar da take  tashi daga waje ne yasa Hindu saurin gyara mata rufin veil ɗinta a fuskarta tace nasan yanzu su Aunty sadiya zasu shigo,tana tufe baki kuwa guɗarsu ta cigaba da ƙuwa zuwa ɗakin Umaimah.

Fita sukazo sukayi da ita a yayin da manya ke binta suna ta faman feshe ta da turare har suka kaita gurin  da aka tanada domin zaman ta,

Ruwan kyalkyali mai kamshi aka fara mata kamar Ba gobe,a yayin da ake binta ta da turare mai Arnen kamshi ana feshe ta ta ko ina,

Kowa cikin matan duk wadda zata fesa mata perfume sai ta aje kuɗi ko wani expensive jewelry

ɗin cikin kwaryan dake gefen ta,

Abunka da Aure na masu kuɗi wanda yazo da Al'ada Kowa da kalar bajintar da yake san Ya nuna har da su hajiya waɗanda basu ƙaunarta ko kusa,amma a wannan rana dole suyi pretending ,dan hatta hajiyan gold ta aje wanda babu wanda yasa Mai tsadar nata,

Jerin motar da suka fara shigowa ne ya sa hankalin mata masu guɗa Ya karkata kan zuwa kamo ango Ya fanshe fuskar matan sa,

Cikin farar shaddar sa da tasha aiki jikin babbar riga ya fito,

Kansa ɗauke da zanna buƙar Mai bala'in kyau fara sai kafafun sa sanye cikin dolchs Halfcover shoe offwhite,abu ɗaya yake ihu a jikin Paki wato MONEY MONEY,

Shine abunda jikinsa ke kira domin hatta agogan dake hannun sa pure diamond ne,

Gefen sa KB ne da abokanan su waɗan da suka sha gayu iya gayu,

Ƙanwar Dada ce taje ta kamo hannunsa tana Mai fadin maza je ka nemi Albarkar manya ka buɗe mana fuskar matar ka 'dan kai ɗaya ake jira,

Cike da fara'a irin ta angon da Ya samu abunda yake marari Ya nufi manyan Umaimah ya kwashi gaisuwa Kafun Ya nufi gurin amaryar sa domin buɗewa kowa fuskarta mai tsada Ya ganta,

Sanin Al'adar yasashi zuwa da shirin sa "Diamond ring wanda yayi worthing maƙudan kuɗi Ya ciro a cikin ɗan kamin box Ya kamo hannun Umaimah wanda Ya gaji da haɗuwa da lalle Ya zira mata,"Tafi gurin Ya ɗauka da guda a yayin da Ya karbi stick ɗin da ke ɗauke da gashin ɗawisu Ya ɗaga fuskar gyalenta,

Wani irin ajiyar zuciya Ya sauke lokacin da idanunsa sukayi tozali da kyakyawar fuskar umaimahnsa Mai rikita masa dukkan tunaninsa,

Gam ta rufe idanun ta amma kan fuskar ta ɗauke da murmushi,

Ɗurkusa yayi dai dai saitin kunnenta yace "babyna ki buɗe idanunki ki kalli Imam ɗinki kisa idanunki cikin nawa dan yau ni dake mun zama mata da miji,"

Buɗe idanunta tayi according to umarninsa,

Murmushi yayi yace"kin gaji da yin kyau matata,kaf a duniyar nan babu mace da take kasheni da raina kamar ki,yau kin bani Aljanna a duniya,"

Babu abinda take sai murmushi dan kyan da paki yayi Ya gama tafiya da ita sanann ga wani ƙwarjini da yayi mata wanda yasata neman magana a bakinta ta rasa,

Horn ɗin da aka hura ne Ya kawo conclusion na ceremony din a yayin da aka cigaba da sauran Al'adu cikin farin ciki ga waɗanda suke yi da gaske,

Da dare Wurin 8,daddy Ya gama jaddada mata nasihan sa wanda ba shine karo na farko ba ,hakazalika yaya Abubakar sai hajiya wadda tata nasihar izgilanci ne dan maganar farko cewa tayi"zamu fara irge kuma yaushe za'a ƙarkaɗe maki ɗakin ki."

Kasa mata shiru tayi dan haka ta cire kunyar wai ita amarya ce tace "Idan mun kawo ziyara kam hajiya dole a kakkab'e tunda bayan kwana biyu shatu da yarana zasu bi bayana ,a kula mana Kafun mu zo gaishe ku.".

Hajiya na shirin mayar mata da zagi daddy Ya shigo ɗakin.

Yaya Abubakar ne Ya tuƙa motar da aka kai Umaimah gidan Paki,

A cikin gidan su ginin da zasu zauna sabo yake wanda aka zubawa kayan alatu sannan babba Mai zaman kansa ,

Idan aka tsaya zayyane maka Ya sashen Paki yake sai ka buɗe baki,dan guri aka buga kamar baza'a mutu ba,

Bangaren su Ummu aka fara kaita amana Kafun aka maido ta sashen ta.

Bayan kowa Ya watse sai Ya zamana daga ita sai Hindu wadda ta tsaya zaman jiran a rako ango ta Kama gabanta ,irin shaƙiyancin da ta ringa ma umaimah har sai da tasa ta fara Jin kunya ,ganin hakan yasa Hindu ta cigaba da kwasarta yarda ranta yake buƙata.

Wuraren goma aka rako Paki ɗakin matar sa,

Babu wani b'ata lokaci bayan dukkan wani abu da Ya kamata ayi suka Kama gabansu yayin da Kb Ya mayar da Hindu gida suka tafi suka barsu da fatan Alheri .

Awkwardly Umaimah ke zaune kan gado kamar yau ta fara Aure tana mai Kallan paki wanda Ya zauna kan stool Yana Mai binta da ido kamar Yau Ya fara ganinta,

Cike da kunya tace "na chanja maka Kama ne ranka Ya daɗe Paki?"

Tasowa yayi Ya hawo kan gadon da take daf Da ita Ya kama hannun ta yace "Alhamdulillah

,ko yanzu na mutu na koma ga ubangijina bazan mutu ina Mai dana sani ba dan Ya bani kyauta mafi mahimmanci a rayuwa ta,"

Hannunta Ya kama Ya ɗora a sautin zuciyarsa yace"kin ji yarda zuciyata ke bugawa saboda ke,kilan ke baki jin yawan Abinda nake ji ,amma dan Allah umaimah ki soni koda kwatankwacin karamin farcen ki ne,ki rike ni amana saboda akan ki ni kaina bana gane kaina.

Kallan sa take cikin ido tana tunanin abun Alherin da tayi Allah Ya azurtata da Paki,

Da Murmushi ta cire hannunta kan saitin zuciyarsa ta Kama hannunsa cikin lallausan nata cikin wani salo na ƙauna tace"wane Ya faɗa maka bana sanka?

Zuciyata duk wani bugu da Zatayi da sunan ka take bugu mijina,ina mutukar sanka sannan zan kula da kai nayi maka biyayya na kyautata maka ,insha Allahu bazan baka damar kuka dani ba,duk da ɗan adam Ajizine shiyasa nake san tun yanzu ka yafen laifin da zan maka cikin sani da kuma rashin sa,

Faɗaɗa murmushin sa yayi yace"indai nine zan ɗaga maki ƙafa ki shiga Aljanna ,na ɗaga miki matata sannan na yafe maki duk abinda zaki mun sane da rashin sa."

Cikin jin daɗi tace"nagode mijina ,Allah Ya barmu tare,".

